********************** ⬇ **************************
********** Ai Hausa Novels ****************
************************* ⬆ **********************

DOWNLOAD More complete Hausa Novels, Education Books, Adventure, Drama, Mystery, Religion, Fiction, Non-Fiction, Romance, Meimor, True Life Stories & Others from our blog.

Visit > https://www.aihausanovels.com.ng

Ka tura mana sako ta adireshinmu na email, domin tuntubarmu ko turo mana hausa novel ko kuma post.

Email > aihausabooks@gmail.com

******* FOLLOW US ******

Facebook: Ai Hausa Novels

Twitter: Ai Hausa Novels

Telegram Channel: https://t.me/Aihausanovels

WhatsApp Number: 08138873799

Haka kuma domin shiga kowanne daga cikinsu za ku iya ziyartar shafin ku yi search na AI HAUSA NOVELS, hatta facebook group dinmu ma za ku samu.

********************** ⬇ **************************
*************** Ai Hausa Novels ****************
********************** ⬆ **************************

[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣

Anatse yayi sallama yashiga wani babban falon wanda suke kira da Shakallo dan sirri kadai kesa a shigo cikin falon, wani irin kirar samfarin gini akama dakin kaman wani museum, yanada fadi da kirma dakin ga wasu ado na gwalagwalai sai babban carpet daya lullube ko'ina a girman falon, sai filoli na tumtum dasuke jejjefe akan carpet din na kishingida anmai ado na sarauta a jikinsu.
Mutane biyar ne zaune a falon maza hutu sai mace tsohuwa guda daya, Mai Babban daki wacce take tsohuwa ta manyanta dan akalla zatai 76 da idanunta sukai jazur tana sanye da Alkaybba hannunta rikeda tissue dakuma charbi tanaja, sai Waziri, Wambai, Makama dakuma Sarkin dawaki, chan kuma saiga wasu Manyan dattawa maza guda biyu dake kama da Mai Babban daki sun shigo sun zauna suma, dan faduwa gabanshi yayi dan haduwan mutanen nan wanda bayan sarki sune masu fada aji a fadan nan kasan babban abune, karasowa yayi tsakiyan dakin sannan yasami waje yazauna yakalli Mai Babban daki yace “Gwaggo kene kika aika akirani”? Girgiza kai tayi kafin ahankali tasa tisssue saman fuskanta tashare hawayen tasss sannan tace “aminan mahaifinka sukasa akiraka amatsayinka na babban dan sarki Kabeer” dasauri yadagokai yakallesu sauran jama'an dakin dake kallonshi yace “tooh” anatse babban cikinsu Makama yace  “kannenka duka sun iso? Dan karfe hudu zamukai Sarki makawancin sa” cikeda kamala dakuma natsuwa yace “Yarima Halilu, Ibrahima, dama suna nan, Munir yanzu yakirani jirginsu ya sauka a Abuja, shikuma Umaru yanzu haka jirginsu yatashi daga lagos din shikuma…..” yay dan shiru, atare dukansu yan dakin sukace “Yarima Riyad fa”? Adan hankali yasauke yar boyayyen ijiyan zuciya yace “nakirashi ba adaddi bana samunshi” salati mai Babban daki tasaki tace “bantaba ganin gantalallen yaro irin Riyad ba, yau yana Egypt, gobe yana Cyprus, jibi yana Oman gata yana zanzibar, citta yana China ko Iceland, ohh ni Shatu, chanake yau yana France ka gwada number shi ta chan kuwa Dan Buri? Idan baka da number kaje wajen Fulani ka amsa” cikin murya mai laushi Dan buri (Kabeer) yace “Gwaggo kema kinsan baitaba yin cikakken wata daya agari dayaba yabarta yatafi wata, kuma har ita mahaifiyarshi Fulanin batasan inda yayi ba dan nasameta itama tana kiranshi baya shiga, ni narasa mecece matsalan Riyad da ya gwammace yayta yawon duniya daya zauna akasarshi inda aka yankemai cibiya, ya girma baisan…….” Hannu sarkin Wambai yadagamai yace “ya isa” yadan sauke ijiyan zuciya yace “yanzu dai sabida shi bazamu jinkirta yima sarki abinda yakamata ba, nasan duk inda yake aduniyan nan zaiga news na rasuwan mahaifinshi dan haka zamu ganshi, yanzu tashi katafi” tashi yayi ahankali yamike yawuce yafita yanajan dan tsaki aranshi bayan yakai waje.
Cikeda bacin rai daya daga cikin jama'an dake falon yace “Gwaggo I've said this time without number to Mai Martaba he should call Riyad to order, duk cikin yaran Sarki babu gantalalle kaman Riyad, yaki zama ya koyi komi na al'addun mu, yanzu me za'a gayama jama'a akaga shine kawai bayanan” kowa na dakin binshi yake da kallo sai dayan dake kusada shi da ake kira da Usmanu yace “a'a Yaya Riyad yarone mai natsuwa dukanmu nan munsani sana'o'inshi ke kaishi kasashen nan kuma Mai Martaba shiya ya aminta da hakan ya bashi go ahead tunda yaga yaron nada passion for business, Riyad yaro ne mai matukar kyawun hali ga tausayi dukkan mu anan munsan da hakan” cikeda zuciya yace “kai ina magana harka isa kabani amsa Usmanu” cewan yayan da ake kira da Hambali, zasuhau gardama Mai Babban daki tace “shup! Hambali Usmanu kunsan dan uwanku ya rasu kuwa? Fada kuke kokarin yi sabida danshi?”

Shiru duk sukayi basu kara magana ba…

Direct flat din mahaifiyarshi Dan Buri yayi wacce take uwargida, wani irin babban gidane da is as if daga inda yake zuwa side din zaije wani anguwa ne, kana ganin Masarautan kasan akwai kudi bana wasaba, dudda ga mata ana koke koke bai hanashi yawuce su yashiga cikin flat dinsu ba. Tana zaune tsakiyan mabiyanta tana kuka yamata alamu da idanu datazo yayi sama, mikewa matar da akalla zatai 48yrs tayi tana gyara lullubi tabishi idanunta sunyi jazur, dakinta yabude kofa yashiga dasauri itama tashigo yamaida kofan yarufe yana manna key, cikin rage murya irin ta munafukai kaman ba itace ke kuka afalo yanzun nan ba tace “ya akayi? Me suka cemaka” Dan murmushi yayi yace “har yanzu ba’a sami Riyad awayaba Mama, abin yamin dadi” dasauri ta dunkulle hannu tawani watsa a iska tace “da kyau Alhamdulillah! Nifa dama Riyad ne kadai matsalata Dan buri dan duka yaran sarki kafisu kudi, kafisu ilimi sannan kafisu connection, gaka kafito daga tsatso mai kyau tsatsona, kuma kai akafi sani afadan nan, Riyad shikadai ne zai nuna maka arziki dakuma kwalin karatu tunda yanada PHD yanzu, amman banda haka meyafika dashi yaron da ko mata baidashi anata gulma ma ana cewa ba lafiya gareshi ba yanda yaki yayi auren nan, kowani Bafade ko jama’an Babbanka za’a tambaya wasukafi so yazama Sarki kowa cha zaiyi kai kai akafi sani kaine jagoran gidan nan kuma dan sarki na fari kasha kuruminka kaman kazama sarki kagama, yanzu dai bari a bunne sarkin anjima dakaina zanje wajen Mai Babban daki anjima, banda Riyad Baffanku Hambali shine mayen kujeran kuma zanyi komi na kaudasu, yi maza wuce katafi waje sabida jama’a su ganka ashaidaka, duk wani kaninka ko kanwarka dazasu iso ka tsaya ka rungumesu kanuna musu soyayya, kazama kaine tsaye akan komi kana kula da komi kaji hakan zaisa kasake farin jini, yanzu tafi tafi ko me ake ciki kadinga fadamin kodako awayane kaji, Mai Martaba yariga ya garzaya saidai kuma mu hadu alahira Mulkin nan kuma tun kafin akaishi makwanci zan fara shige da fice saka akai, kaine d’ana dan fari kaine kuma magaji” Murmushi yamata sosai harda dan dariya yace “Mama kinyi ne arayuwa” da sauri ta shafa fuskanshi tace “kaga daina nuna farin ciki yi fuskan nan ne kaman kai kadai akama mutuwan nan agidan nan” gyadamata kai yayi yakoyi sakwa sakwa da fuska uwa zai fashe da kuka nan ko ranshi fess yawuce yafita daga dakin.

Komawa yayi waje inda dubbanin jama’a suka taru ga kannenshi su Halilu, Ibrahim, Shu’ibu duk sun iso da Iyalansu da akai cikin gida dasu Munir shine last person daya iso wajajen yana zuwa wajen da Babban wan nasu ke zaune yayi cikin jama’a tareda yayyinshi kafinma ya gaidasu yace “Dan Buri kasami Riyad?” Girgizamai kai yayi kaman salihin nan yace “no tunda kun iso yanzu za’a sallaci Baba bazamu jirashi ba kodama yana hanya ne sabida shi bazamu bari Baba ya kwana ba” Munir baice komiba yajuya yafito zuwa wani waje da ba mutane sosai yaciro wayanshi yashiga kiran Riyad danko jiya sunyi waya wuraren 1 nadare but numbershi baya shiga yanzu harzai maida wayan kunnenshi kaman wanda yatuna wani ba yashiga email nashi ya aikamai sako sannan yawuce yakoma ciki akai Alwala aka sallaci mai martaba aka bunneshi nan cikin fada.
Magana sai yawo yake kan duka yaran sarki sun sallaci mahaifinsu banda Yarima Riyad dan Sarki na biyar cikin yaran sarki maza guda shidda ran Dan Buri fess har wani kara haskakawa yake jin yanda rumors din ke flying.

Cikin gida Munir yashiga tareda yayyinsu zuwa babban falo da duka matayen Marigayiya Sarki ke ciki kowacce zaune sanye da hijabi idanunsu jazur ga yan uwa da abokan arziki duka aciki, wajen Fulani suka fara zuwa dukansu yaran anatse suka gaisheta amsa musu tayi suka wuce wajen Fulani 2 suka gaidata itama ta amsa su suka wuce wajen ta uku itama ta amsa ta hudun suna gaida aka dan zauna akai addu'a aka shafa sannan suka fice suka koma wajen maza dan karban manyan baki top politicians manyan kasa from across the world.

JOIN INTIMACY CLASS TODAY WITH JUST 5k MY PEOPLE LEMME TEACH YOU YANDA AKE HAVING AMAZING LOVE MAKING DA YALLABAI! YANDA AKE ENJOYING SEX! YANDA ZAKI TASHI KANSA KIKUMA KWANTAR MAI DA HANKALI.
YANDA ZAKI KWANKWANCE KAN MEGIDA DA MAGANAN BANZA🔥

I AM THE BEST IDAN DAI HARKAN KARATUN NAN NE A HAUSANCE😎

Chat me up wa.me/+2347012181461
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

EPISODE2️⃣

✍🏻M SHAKUR

Kusan gudu gudu, sauri sauri yake tafiya acikin airport din bai damu da bala'in gajiyan dayayi ba sabida economy ticket yasamu bama business ko first class ba, tunda aka haifeshi yaune first time daya taba flying economy, kafafunshi sun sandare abunka da mai tsawo sunma kumbura.
Fitowa yayi daga arrival yafara tafiya dan zuwa wajen parking motoci wasu mutane biyu biye dashi abaya dake sanye da suit bakake da glasses akan idanunsu, lift yashiga harya danna 2nd floor kofan zai rufe mutane biyun suka sako hannunsu ciki kofan yakoma yabude dan dago kanshi yayi yaga wani black mutum ne yana sanye da suit baki ga wanima exactly irin kayanshi suka shigo elevator din suka danna boturin dazai rufe kofan, kofan yarufe yafara moving sama, dauke kanshi yayi daga kallonsu yadaga hannunshi dake daure da agogo na Rolex dan duba karfe nawa yanzu hakanan yaji bai natsuba amman yadake yana tsaye inda yake rikeda bag pack din dake rataye shoulder nashi that is very fine and unique dan babu kalan su ma a Nigeria, hannu daya daga cikinsu yakai ya danna lock elevator ya tsaya chak tareda juyowa yana zaro wani wuka daga bayanshi in seconds yakai zai chakamai aciki chak Matashin yarike hannunshi yana kallonsu cikeda fargaba da tsoro da komima, dayan mutumin shima yaciro tashi wukar yace "au gardama zakayi bazaka bari mu kasheka ba salin alin mu karbi ragowan payment dinmu" shima yaciro wata karaman wuka zai chakamai kwasheshi yayi da kafa yafadi akasa wukar tafadi zai dauka yatake hannunshi da boot din kafanshi, yawani lankwasa hannun

wanda yarike tareda sa kafa yadakeshi a balls dinsa cikeda azaba gayen yayi ihu yayi baya yakama gaban wandonshi yanaji kaman zai mutu da sauri guy din yasa hannu yabude kofan elevator din baimasan wani floor bane suke kawai yafice dagudu gudu sauri sauri dayan dake kasa yatashi yace “call the rest bari nabishi” yafice yabar wanda ke rike da gaban wando yana kokarin kiran waya, yashiga gudu shima yana binshi abaya, sosai yake gudu ganin daya yabiyoshi yanakai hannunshi cikin wando dan ciro wayanshi yakasa kawai yahau staircase yashiga sauka yana kallon baya jin gudun sahu dayawa ana biyoshi dudda baya ganinsu dan basu riga sun hayo benen ba ganin wani kofan restroom na mata dan ansa ladies ajiki yasa kawai yabude kofan yafada jiki wani kalan mugun karo sukaci dan tana shirin fita ne tai tangal tangal zata fadi da bala’in sauri ta dafa bango shikuma yajuya ya tura kofan bayin dasauri tareda saka sakata na sama da kasa yana kara murza jam lock sannan yajuyo daidai tana dagowa tana shafa goshinta cikin tsananin fushi dan tadan buge kuma taji zafi zatai magana, cikin a very soft yet anxious voice guy din yace “please ki boyeni some guys naso su kasheni ne and call the police” dudda taji zafin bigewan datayi amman ware manya manyan dara daran idanunta tayi kaman fitila tana kallon mutumin dayashigo cikin bayin mata da ranan nan Allah yaso ba kowa ciki ma, farin guy ne bawai irin fari sosai dan zata fishi haske but yanada normal fair skin not black skin, dogo wanda akalla zaiyi 34-35 ko 36yrs hakanan, baida kiba at the same time baida rama, yana sanye da riga na latest collection na Dior fari yadaura wani leather brown jacket asaman sa da yabar boturan abude bai rufe ba hakan nasa kana ganin farin rigan ciki, saikuma yasa  jean na Rick Owens, sai wani boot dake kafanshi brown na Tomford mai bala’in kyau da agogo daure a writs nashi na rolex, yanada very very dark hair dake nan kwance so wavy, dark eyebrows da eyelash nashi yamafi na wasu mata yawa, ga dan gemu dayake dashi da saje acike dudda gemun baida tsayi sosai looks like yana trimming gemun dan hair na wajen gabaki daya na dsame length, lips nashi are full irin asalin masculine lips that are a bit pinkish, idanunshi sunyi jaaa sosai, ganin yanda take kallonshi yasa yace “call security” hankalinshi atashe yadanna kofan da hannunshi yana kallon kofan jikinshi nadan rawa kana gani kasan da gaske he’s in trouble jin gudun mutane dayawa haka ga maganan su yana tashi kasa kasa “baku ganshi ba? We have to kill him ance kar mubari yakai gida araye wannan kofan fa kunduba ciki ko ya boye wajen”?  Hankalinshi atashe yajuyo yana dan zaro idanu hakan yasa itama gabanta yafadi bayin tashiga kallo kafin idanunta su sauka kan cart din garbage can dake wajen wanda take juye dattin bayi aciki ta gungura tafito dashi takai bola, daga kafanta tayi without making sound taje ta tsaya kusada can din tasa hannunta ahankali tabude marfin sannan tadago kanta daidai sun fara knocking kofan zaro idanu yayi da sauri ta nunamai can din da hannu alamun yazo yashiga nan da sauri yazo ya tsaya kusada ita yakalli bolan cikin can din wani kalan yatsinewa cikinshi yayi yaji kawai amai yatasomai da sauri yadaura hannunshi kan bakinshi jin aman zai fito, tazaro idanu tana kallonshi yau da babuma wani bolan kazanta sosai ma shine zaiyi amai lallaima, daidai an kara knocking dasauri da murya kasa kasa tace “kaga idan bazaka shigaba nifa ba ruwana, kafita ni nacigaba da aiki na, I don’t have any security number I don’t work here yau kawai an kirani nai replacing wata ne just for today” juyo da kanshi  yayi yakalleta itama kallonshi tayi da manyan idanunta kusan iya kirjinshi tsayinta ya tsaya daidai anyi mugun knocking kaman za’a balle kofan baisan lokacin dayay tsalle yafada cikin trash dinba yasa hannunshi yana kama hancinshi lekowa tayi takalli ciki yanda yakeyi yasa tai dariya dayasa fararen  hakoranta suka bayyana more of dariyan

mugunta tace “yi bacci toh” kallonta yayi yanda take dariya dimples nata na lotsawa bama ta tsoro yanda kasheshi akeso ayi, bama ta tsoro tana mace itama sujimata ko su illatata, he’s just staring at her da suprise, jakanta dake kan slap ta kalla saita wuce da sauri tabude taciro wani black gyalenta na abaya tazo wajen ta warware ahankali ta yafa kanfuskanshi, wani irin lumshe idanu yayi jin kamshi mai sanyi daya sauka kan fuskanshi mai ni’ima in this moment na wari dayake ciki sai kuma ya sauke gyalen da sauri ya kalleta yace “wat are you doing?” Tana kallon kwayan idanunshi itama ba kunya ko shakka tace “datti zan watsa akanka yanzu so brace up” takai hannun tadauki thrash can dake kasa wanda bata riga tajuye dattinshi ba kawai tajuye asaman kanshi tana murmushi ganin yanda yake kallonta kaman zai rufeta da duka tace “I am saving your life here it’s your choice” wani kalan ijiyan zuciya yake saukewa tsigan jikinshi natashi da kyar yaja gyalenta yarufe fuskanshi dashi yana rufe idanun duka dan yakasa standing dattin datake watsamai akai ta ijiye can din tasa hannunta dake sanye da working glove nata ta kwashi sattın ta rurrufeshi da kyau sannan ta rufe marfin tadan sauke ijiyan zuciya cike da karfin hali tawuce tai wajen kofan tabude cikeda masifa tace “wai waye ke knocking haka ina aiki”? Ganin maza kusan biyar yasa tadan koma baya kadan ta tsaya chak tana kallonsu dudda gabanta na faduwa bata nunaba dukansu kallonta suke ganin wata yarinya da akalla zatai 22yrs haka tana sanye da cleaners uniform riga da wando ash color tasa wani karamin farin hijabi daya tsayamata iya kirji hannunta sanye da glove kafafunta sanye da rain boot, cikin rashin tsoro tace “baku iya karatu bane duk girmanku ku gane ladies restroom ne nan”? Dukansu kallonta suke ganin yanda take musu magana gata wata kalan kyalkyawan yarinya fara sol saidai akwai uban baki ga rashin kunya ga muryanta shegen zaki kaman zai fasa dodon kunne, babban ne yahade rai yace “ke wani bai shigo nan ba”? Wani kalan matsiyacin kallo tamai tace “kai nan wajen yamaka kama da inda wani zai shigo”? Dukansu baki suka sake suna kallonta daya daga cikinsu yace “ke kinsan waye mu kike mai rashin kunya”? Tana kallonshi tace “kai kasan wayeni zakuzo ina tsakiyan aiki na bayan nayi stating agaban kofa working no entry kunzo kuna bubbugamin kofa kuna maza toh ubanme kukazoyi nan kuje men restroom mana, I will call security wlh” kallonta Oga yayi this loud girl can ruin work nasu ta tara musu jama’a yanda take this vocal ma killing her will never be easy still saita tara jama’a, they don’t want scene hakan yasa yace “please let her be she’s crazy, I don’t want problem, ku rarrabu kuje mu nemoshi ni nasan yana floor din nan” tsaki tayi tace “mahaukata kawai” dukansu su shiddan juyowa sukayi suka kalleta wlh ko dar batajiba tasa hannu ta maida kofan ta buga tarufe tadauki wayanta ta danna waka tamaida earpiece tacigaba da mopping kasan wajen wanda shiya rage mata dama tariga tagama wanke cikin bayukan yanda takebin wakan tana aikinta bata missing any verse wlh zaka dauka mawakiya ce kuma da karfi take wakan abinta.…..

Dudda yanajin warin bolan dayake ciki kaman zai kasheshi ga tsoron dayakeji but hakanan muryanta da yanda take wakan hold on na calming nashi down sosai, muryanta yamafi na asalin wanda yayi wakan dadi, what a voice! Tass tagama aikinta ta jingine komi inda zata jingine sannan tadauki jakanta tarufe tagoya abaya tasa hannu tabude kofan bayin hada ido tayi da maza biyu daketa sintiri awajen ta ballamusu harara tacire board na close dake gaban kofan bayin takoma ciki ta ijiye sannan ta gunguro garbage can din da kyar sabida nauyi amman ta

daure tafita tafito dashi ko kallonsu batayiba saima wakanta data cigaba dayi abinta tawuce tasauka har kasa tazaga baya inda suke ijiye dattin saida ta jujjuya ganin babu kowa yasa tabude marfin bolan batare data kalli cikiba tace “you are safe yanzu you can come out” kafinma ya yunkuro tajuya abinta tahau tafiya dan sauri take is already 3:30 by 4 zata shagon abinci gashi this whole drama yabata mata lokaci, da kyar ya iya ya lallaba yafito daga bolan sai amai duk wani abu dayaci saida ya amayar dashi sai kakkabe jikinshi yake yadago zai mika mata gyalenta daidai tanashan kwana harta tafi, he wanted to say thank u dudda she’s a crazy wicked girl tana zubamai dirt tana murmushi but she helped him, hannunshi yakai aljihunshi yataba but baiji wayanshi ba kuma baisan a ina ta fadi ba wlh kuma shi bazai duba bolan nan ba, daidai wani cleaner na gunguro nashi bolan dasauri yace “please bani aron wayanka nakira” binshi yayi da kallo ganin kaman ba lafiya yasa yabashi wayanshi Munir yakira kafin yayi magana yace “Munir kazo ka daukeni a airport pls karka fadama kowa kana zuwa katambayi wajen zuba bola ina wajen” kafin yayi magana ya katse wayan yabama yaron yazauna awajen kawai feeling terribly sick kusan 1hr yana wajen  jikinshi yadau mugun zafi ga tsigan jikinshi na tashi kaman zai mutu yana zaune ahaka yaji ance. “Riyad” dasauri yadago kanshi da gudu gudu sauri sauri Munir yataho wajen yace “what happened to you like this? Wat are you doing here? Why are you so dirty”? Tashi yayi yana kokarin yima Riyad magana yace “someone tried to kill m…..” kawai ya sume da kyar Munir yasamu wani cleaner yazo kawo datti shima aka tayashi daukanshi suka tafi mota aka sashi sai gida bayan yakira Mom akira Dr.

Tawani special secret gate Munir yabiyo aka budemai already ga mutane tsaitsaye Gwaggo (Mai Babban daki) gawata black beauty mata dake sanye da hijab mai dan kiba (Mom), Wambai, Waziri, Kabeer da su Halilu, Ibrahim da Shuaibu, Baffa Mujitapa dukansu suna wajen da family Dr nasu, yayi parking agurguje Munir duk sukai wajen fashewa da kuka Mom tayi tace “what happen to yarona Munir? Wakeson kashemin shi daga shigowanshi garin nan? How did they even know ya shigo? Gwaggo jini a hannunshi look, Doctor do something” Mom tai maganan tana kama hannunshi ashe wukan ta yankeshi dazu, atare dukansu mazan suka ciccibeshi zuwa wani dabkareren flat na Mom Gwaggo tace “meya sameshi haka Munir? Jibi jikinshi? Meya faru Munir”? Dasauri Munir yace “Gwaggo nima bansani ba but kaman he was attacked ne, yana kokarin fadamin wai ana kokarin kasheshi ya sume ba wayanshi taredashi, shi babu akwati, akusa dashi, awajen bola naganshi da bag pack yana mota dawani dan kwali black, kafin yafadamin komi kuma yasuma” gam Mom tarike hannunshi har daki kan wani taskeken gado aka kwantar dashi Dr yashiga dubashi yanda skin nashi da fatanshi keyin wani bororo dahar wani motsi suke yasa yace “a chanzamai kayan jikin nan nashi maza, ku goggogemai jiki with clean towel, allergy ke damunshi, he’s allergic to dirt da kazanta right from small, kuyi sauri pls” fita kowa yayi daga dakin akabar Munir da Mom, Waziri da sauran duk suka zauna a falo yace “wazai attacking yaro daga durowan shi kasan nan?” Anatse Wambai yace “call the police I think sai anbincika airport din maybe ta CCTV za’a gani” faduwa gaban Kabeer yayi amman yadaure yaranshi always do a clean job he hope bazasu kwofasashi ba, fitowa Munir yayi yace “Dr an gama” dukansu komawa ciki sukayi Kabeer sai tsaki yake aranshi shida yakeso kowa yaji haushinshi amman jibi yanda kowa ke nan nan dashi, attention yakoma kanshi ma infact, skin nashi gabaki daya yakoma so red, drip akamai fixing da allurai ciki Dr yakalli Mom datafi kowa damuwa adakin yace “anjima kadan zai farfado don’t worry” dan

murmushi tayi tareda gyadamai kai Waziri yace “ki zauna dashi” Gwaggo tace “nima ina nan kome za’a kawomai kowa zaizo yadubashi saina ganshi inga uban waye keso ya cutar mini da jika, bangama kukan mutuwan d’ana ba yanzu halakamin jika za’ayi wlh jinina yasha karfin kowa” kallon Munir Mom tayi ahankali tace “thank you Munir” gyadamata kai yayi yawuce yafita daga dakin hakan yarage daga Gwaggo sai ita, dafata Gwaggo tayi tace “ki tsare yaron nan ki dage da addu’a akanshi, tun ranan da aka haifi Riyad akace yanada taurari masu kyau kuma babban mutum ne shi, kiduba kigani yaran marigayi maza shidda amman shi kadai akeso ahalaka tun yanzu kenan bama asan waye zai gaji kujeran sarautan ba kenan amman so ake akasheshi balle kuma ace shine zai gaji sarautan ki tashi tsaye Maryama, saikin tashi tsaye, kinyi zaman gidan nan basai na fadamiki hadarorin dake cikinsa ba, inde kalubale ne yanzu Riyad yafara gani, idan kuma yazama Sarki yadinga ganin kalubale iri iri kenan har abada, ki tsare yaron nan, kizama idanunshi kunnuwanshi uwa uba kizama inuwarsa dakuma lullubinsa” gyadama Gwaggo kai Mom tayi takama hannun Riyad tarike gam tana kallonshi tace “Gwaggo meya musu Riyad dako zaman gidan nan baiso, na tabbata baimason ya gaji kujeran nan, dan bata gabanshi” Gwaggo tace “kwarai” Mom tace “shi kadai Allah yabani, shi kadai gareni, Riyad kadai Allah yabani yau ana kokarin rabani dashi” kankame hannunshi tayi tace “Gwaggo zan iya zuwa bangon duniya sabida Riyad! Kuma nayi alkawari duk Wanda yace zai cutar da yarona saidai yafara dani dan daga yanzu zan zama shamaki tsakanin Riyad da komi na duniyan nan, zan zama inuwa hazo zan lullubeshi nakuma kareshi daga duk wata hari” sosai Gwaggo take kallonsu sai kawai tai murmushi tadauki charbi ta tacigaba da ja itama bini bini tana tofama yaron addu’a aka.

JOIN GROUP DANAKE POSTING NOVEL DIN NAN

https://chat.whatsapp.com/CrKHphXCxK09RvYbrO1cCU
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

EPISODE3️⃣

✍🏻M SHAKUR

WHEN WAS THE LAST TIME KIKA SAYI SABON PANT?🤭 TALK TRUE

BRA DINKI SUN KOMA RUWAN KASA TSABAGEN SAWA KULLUM😒

TO IDAN NACE YAU NAKAWO MIKI HABISHMA UNDERWEARS FA👙💃 SUNA SAIDA PANTS, BRAS, NURSING BRA, MATERNITY GOWNS, NO LEAKAGE PANTS NA PERIOD, KAYAN BACCI DA SAURANSU🔥

SUNADA MOST AFFORDABLE KAYA GA VERY CHEAP DELIVERY NATIONWIDE GO AND BUY NOWWWW!!!

https://www.tiktok.com/@habismaunderwears?_t=8lzVAMnAhgk&_r=1

4 daidai tashiga wani babban kanti na abinci irin local restaurant din nan, wata katuwar mata dake zaune a tsakiyan shagon kan kujera ga lalitan uban kudi a hannunta tana kirgawa ne ta kalleta tace “Allah yasoki baki latti ba” batace komiba kai tsaye tace “ina wuni Maman Miwa” batare data amsaba tace “nidai je ga wanke wanken ki chan na jiranki” bata damu da yanda tamata maganan ba dudda akwai mutane a shagon sunacin abinci tace “bari nai salla naje nayi” bata jira amsanta ba tawuce ciki chan bayan gidan shagon bayi taje tacire kayan jikinta tafito da dogon riga na abayan dake jakanta tana neman gyalen ta tuna tabawa mutumin nan tsayawa tayi chak sai kawai taja gajeren tsakiya saurin datake tazo nan yasa ta manta bata amsaba, karamin farin hijabin tasaka ta dauro alwala tafito tasami waje tai salla sannan ta cire hijabin tasa kan igiya fari ne batason ruwan wanke wanke ko mai ya bata mata taje gaban makwarara, ga wanke wanke zaka dauka na gidan biki ne ga manya manyan tukunyan abinci, omo ta dauka ta tara ruwa abaho dukta kawo sannan ta dauki wayanta kirar vivo duk taci screen tasaka earpiece ta danna waka ta soke wayan aljihun dogon rigan tashigayin wanke wanken da sauri sauri dan tanada kuzari sosai batada kasala ko son jiki.
Wata yar budurwa ce tazo wajen ganinta tana wanke wanke tana waka kasa kasa like zero worries dinnan yasa ta harareta tajuya tafito tadawo cikin shagon tazo gaban mahaifiyarta dahar lokacin take kirga kudi tace “wai Mama Yar gidan HIV dinchan kikesa take mana wanke wanke har yanzu banace ki sallameta ba gashi gashi abinda ake cewa ita da Mamanta sunada shi” batare da maman ta kalletaba tace “koyar gidan kanjamau ce ba HIV ba ina ruwana ko kinada wanda zaki samo dazatamin wanke wanken nan ta share ko’ina har zuwa katon shagon nan akan dubu biyu kullum aduk fadin garin kanon nan?” Baki yarinyar tabude zatai magana Maman Miwa tace “kinga ki kyaleni fa, nagadai nace kiyi aikin nan bayi zakiyi ba” dasauri yarinyar tace “Mama ni kyamanta nakeji wlh, sunada HIV tana mana wanke wanke” dasauri Maman Miwa tace “wai sau nawa zan gayamiki Maman ta kedashi ba itaba yarinyar datake karatun likita, to koma tanadashi me ruwana nagadai ciwon nan ajini yake kuma baya kwarara acikin ruwan wanke wanke ko? Miwa dan Allah ki barni na kirga kudin nan kinatasa ina mance abinda na kirga” tsaki yarinyar tayi tawuce tafita daga shagon cikeda bacin rai.
Kafin 1hr tagama wanke wanken nan tass, tukunyoyin har bayansu ta wanke kal sai kyalli suke ta share ko’ina tashigo shagoma ta share tsaf tai mopping lokacin biyarda rabi sannan takoma baya tasa hijabinta tadauko jakanta ta goya abaya tafito tazo gaban Maman Miwa tace “nagama” kallonta Maman Miwa tayi tace “ohh kudinki ko”? Gyadamata kai tayi, kudin hannunta Maman Miwa tashiga kirgawa taciro 10k tabata tace “gashi na litinin zuwa yau juma’a” murmushi tayi for the first time dan gaskiya she hardly smile kaganta tana murmushi ko dariya to sai in tana tareda Mamanta, takirga kudin tass dubu goma chip chip tace “nagode Allah yabiyaki” tajuya tawuce kallo Maman Miwa tabita dashi ance duk muguntan ka kaji an maka wani addu’an saikaji ranka ya sosu harta fita waje Maman Miwa tace “Rasheeda!” Dasauri yarinyar tajuyo jin an kirata, komawa cikin shagon tayi tace “na’am gani” kallon sales girl dinta Maman Miwa tayi tace “samata shinkafa da tuwo a takeaway takaima Mamanta” wani kalan

murmushi tayi dayasa wani hot dimples suka lotsa a kumatunta Ya Allah! She looks damn beautiful dasauri tace “nagode sosai, nagode nagode” Maman Miwa sai kallonta take dan wlh today is the first time in almost 3months data fara musu aiki take ganinta tana murmushi, yarinyar kam badai kyauba, ta tabbata badan cutan su ba da tuni wani babban Alhaji ya aure ta, kawomata abincin akai a leda ta amsa wannan karan saida ta duka tace “nagode sosai Maman Miwa” murmushi Maman Miwa tamata tace “sai Allah yakaimu  gobe” gyadamata kai tayi tafice Maman Miwa tabita da kallo wani zubin she wants to be wicked amman kuma indai kai ba shaidan bane u can’t be wicked to this girl cus zata maka aiki tsakani ga Allah dabazaka taba ganin abinda zakai complain akai ba, wanke wanke take maka tsaf, tai shara tai moping kaga ko ina na kyalli, banda haka  daidai da tsinke bata taba sata a shagon ba wlh ko kwayar magi bai taba bataba dudda ko basudashi, kowa ya tsaneta kowa kyaranta yake sabida Mamanta but if u look at it ciwo nakan kowa, zata gudu tabar mahaifiyarta ne sabida tabada HIV? No, ba HIV ba ko HIVVV uwarta kedashi uwarta ce, dudda ma taji labari ance mai kudi mahaifiyarta ta aura but taje tai fasikanci tasamo HIV yakorota yace cikin ma ba nasa bane, hmmm tasauke ijiyan zuciya tace “Allah ya kyauta dai”.

Tafiyan datayi zaiyi nisan tafiyan inda zakaje kabiya 200 ko 300 kan adaidaita sahu amman akafa tai tafiyan nan tana shiga layinsu ta tsaya gaban wani chemist ta kirga 6500 tabashi tace “ga kudin maganin nagode” karba yayi yace “an dawo daga aikin Rashy” gyadamai kai tayi batace komiba ya karbi kudin yana kokarin kirgawa daidai ta juyo zata fito wasu maza guda biyu na zuwa wajen daya daga cikinsu yakalli mai shagon yace “kai Bala nagaya maka idan kana bari yarinyar nan na shigowa shagon ka bazaka taba yin ciniki ba ni nama fasa sayan abinda nazo saya mtswww yawa kake wlh gaye” yajuya harya fara tafiya Rasheeda tace “ko dabba yafi jahilin namiji mara ilimi daraja tirr, adaije makaranta akaro ilimi katon banza” chak saurayin ya tsaya saikuma ya juyo yanuna kanshi yana kallonta kur itama Rashida ke kallonshi yace “dani kike”? Dasauri Mai chemist din Bala yazagayo yana daga marfin kanta yafito yace “badakai takeba Rashida tafi gida kudin sun cika nagode” wani kalan kallo tama mai chemist din tace “akanme zakace badashi nakeba Bala? Inba dashi nakeba waye yamaka kama da jahili awajen nan”? Wani tahowa gayen yayi azuciye zai daketa yace “zan sumar dake wlh ke” dasauri Bala yatareshi yace “me haka kai Sani dukan mace zakayi”? Wani kalan dariyan daru Rasheeda tayi tasauke jakanta dake goye abayanta ta ijiye ledan abincin hannunta duka akasa tanuna kanta tace “nizaka daka?” Tasake dariyan keta tace “billahillazi yauka tabani saidai uwarka ta haifo wani zan gwada maka ni dakake gani kaman maza dari ce anan, try me I will make sure namaka abinda baxaka so ka karabin hanyan danake bi ba” tai maganan azuciye cike da fushi da masifa da rashin tsoro, dasauri Bala mai chemist yakalli abokin Sani yace “please rikeshi ku tafi dan Allah Kamal” kamashi abokin yayi yace “muje Bros shareta pls ba riba a fada da mace” Rasheeda tace “kasan Jahili baida ilimin sanin hakan wannan dahar yanzu ake raba shayin safe dashi agida” haba wani kalan fizge kanshi yayi yakawo mata duka da duka karfinshi kaucewa Rashida tayi da sauri yasami bango batai wata wataba ta daga kujeran dake wajen na zaman mutum plastic chair ne ta rapkamai a fuska kafan kujeran ya yakushi bakinshi haba bakinshi sai jini ganin jini abakinshi yayo kururuwa zaiyo kanta da sauri abokinshi da Bala mai chemist suka rikeshi, itama Rasheeda cikeda fitina ba tsoro azuciye tace “ku sakeshi yazo bakaga komiba duk bakin dazai kokarin bullying dina wlh saina fasa bakin, kai kayi kadan

kahanani sakewa agarin nan sabida ka ganka namiji, akan wani dalili zaku hanani sakat bazan iya zuwa nasai abubu? Shaguna nawa nadena zuwa na layin nan? Wannan danake zuwa yanzu shima kuce ban isaba sabida wani dalilin ku na banza da wofi, cuta nakan kowa, babu wanda yasan karshen shi, yes Mamana nada HIV and so what? Kubi duniya a sannu kai kanka bakafi karfin kasami cutan ba dakiki kawai mahaukaci, katon banza wanda ake gutsurama buredi agidansu har yau akasa dashi da kannenshi sabida baida zuciyan nema, kar Allah yasa ka kara zuwa shagon siyan abu, jahili kawai" cika shagon akayi da mutane sabida yanda Rashida ke zubamai zagi shikuma yana kokawa dasu Bala asakeshi ya daketa ganin yanda ta fasamai baki, cikin taron mutanen wani dan tsoho ya leko ganinta sai kawai ya shigo cikin shagon yakai hannu ya karbe kujeran ya ijiye gaisheshi mutanen wajen sukahau yi. "Barka da yamma Baba Liman" cikeda hikima na manya ya dubi Sani yace "ayakuri Sani, kekuma wuce mutafi" hannunta yakama yace "wuce mutafi" batai musu ba akumbure cikeda taurin kai tace "ni jakata" sakinta yayi yana kallonta taduka tadauki jakanta ta goya abaya da ledan abincin tarike a hannu tana nishi kaman kirjinta zai fashe sabida fushi saikuma ta dago azuciye dan tanada naci wani zubin kaman mayya, takalli uban mazan dake wajen duk ana kallonta tace "Baba Liman kagayama yan anguwan nan su kiyayeni nida mahaifiyata, bamu shiga gidan kowaba munyi sata, Mama harni baya shiga gidajensu sabida yanda kowa ya kyamace mu, bamu rokesu kudi ba, banzo nacema kowa yabani kaza zankai mahaifiyata asibiti ba dan haka su fita daga rayuwata dana mahaifiyata Baba, sufita na gayamusu, I am enough for Mamana! ni kadai zan iya kula da ita, nayi girma kuma Alhamdulillah inada karfin yimata komi kowa yafita harkana, ban nemi fadan kowaba ban shiga hurumin kowaba dan haka duk wanda yashigo tawa koshi waye wlh sai inda karfina yakare kagaya musu Baba Liman" tayi maganan with a sound warning, ahankali tsohon yace "ya isa!" wucewa tayi fuuuuu tafice daga shagon kowa na wajen jikinshi yayi sanyi wani dakeda shago kusada na chemist yakalli yaron yace "kudaina abinda kukeyi mutanen nan ba akanku suke zaune ba, wlh Allah zai iya saka musu, shidai cuta nakan kowa, yau dauka fasikanci matan tayi tasamu Allah masani amman ina mai tabbatar muku, gulma, keta, rashin mutunci da sa'ido da menene menene kukema matan da yarta kadai ya kore zunubansu" anatse Baba Liman yace "muji tsoron Allah, mun kyamaci mutanen nan shi kadai ya isa wlh kudena takura musu kar Allah yakamaku, kar Allah yakamaku" yawuce shima yatafi, dasauri Bala yace "nima kada ka kara zuwan mini shagona kaje wani chemist din" tsaki Sani yayi yace "ka dinga shiganmata ko zaka mutu iyayyenka dai damuka sani bazasu taba barinka auren tijararriyan yarinyar me kanjamau dinchan ba" yayi maganan yana ficewa dağa shagon abokinsa na binsa.

Gidansu na wajajen karshen layin, wani dan karamin gidane sosai ciki da falo daya ne sai bayi ba kitchen a tsakar gidan suke girki, ko'ina kal kal agidan, maida kofan tayi tarufe tasa sakata tasauke ijiyan zuciya sannan tai murmushi dan bataso Mama tagane ranta yabaci daganan zaure tai shouting "Mamaaaaa, Mama nadawo" tai ciki da gudu labule ta daga Maman na zaune kan dadduma kaganta kamansu daya sak da Rasheeda itama tanada haske but ba kaman Rasheeda ba, batada kiba ko kadan ta rame ta bushe sosai, duka duka bazata wuce 40 ba but she looks kaman wacce ta tsufa, tana zaune kan dadduma tanajan charbi, ijiye kayan hannunta Rasheeda tayi saikuma tai tagumi tana leka fuskan Mama tace "Mama kiyi sauri kigama kimin sannu da zuwa niii" tafadi a shagwabe, hannu Ammi tasa ta shafe addu'an datakeyi sannan

tajuyo kawai saita kama kunnenta ta saman hijabin jikinta tace “dan kaniyanki ba alwala yakamata kiyo ba kizo kiyi salla ba” dariya sosai tayi tana yarfe hannu tace “wayyooo kunnina Mama zai cire” sakin kunnin Mama tayi tana murmushi looking so happy tace “imaza to jekiyo alwala kafin lokacin magrib yafice baki salla ba” tashi tayi tafito tsakar gida alwala tayi tadawo tai salla kusada Mama sannan tadauki jakanta tabude taciro kudin tasa a hannun Mama tace “Maman Miwa tabiyani, hotel din nan gobe suma zasu biyani kuma manager tace nakawo zanen tagani idan na iya sosai zasu saya” karban kudin Mama tayi tana kallo tana murmushi Rashida tashiga fito da abincin tace “nabiya nabawa Abdul kudinshi Mama ga abinci Maman Miwa tace nakawo miki” bubbude komi tayi ta tashi tafita dasauri tadauko ruwa a bowl tadawo tazauna takama hannun Ammi tasa aruwan tace “wanke hannun muci” wanke hannunta Ammi tayi ta ijiye kudin agefe ta gutsuro tuwon instead takai bakinta bakin Rasheeda takai dasauri Rasheeda tace “Ammi ke kici” ahankali tace “ni naci abinci namana shinkafa, keko nasan tun safe bakici abinci ba banda karin dakikayi ko kinci wani abu”? Hadiye tuwon bakinta tayı tana fikifiki da ido most of the time idan tana aiki mantawa da abinci take, hararanta Ammi tayi tace “bude bakin, kidena wasa da abinci kinji Doctor” gyadama Ammi kai tayi tana murmushi Ammi nasa mata tuwo abaki tace “ko biscuit ne buy and eat kinji” sake gyadamata kai tayi, haka Ammi tadinga feeding nata kuma sosai taci ita bama tasan takusan cinye tuwon ba saida takalli takeaway dasauri tace “Ammi  nacinye miki tuwon” murmushi tayi tace “haka nakeso dama Doctor” tass tacinye tuwon Ammi kuma taci shinkafan ba sosai ba dan batajin yunwa, sannan ta tashi taje tayo wanka da alwala tareda Mama sukai salla ta shiga tattara yan kwanukan zata wanke Mama tace “kibarshi jekiyi zanen ki zanyi wanke wanken” dasauri tace “Mama ni kidaina aiki, bayawa yanzun nan zanyi nagama zanyi zanen” kafin Mama tai magana tafice daga dakin biyota Mama tayi dudda haka tana wankewa Mama na dauraye wa suka gama suka dawo daki tayata Mama tayi ta kwaso board na zanen da colors nata da pen ta zuzzuba tafara zanen kome takeso Mama na mikamata suna cikinyi aka dauke wuta torch light Mama tadauka ta kunna Rasheeda tai murmushi tacigaba dayi sai wajajen 12 tagama tabarsu su bushe gobe zata sasu acikin frame, zama tayi anan danta huta kafin suje su kwanta sai bacci itakuma Mama na tattare brushes din tana dauraye mata su aruwa, munsharin ta da Mama taji yasa tajuyo takalleta ganin yanda take baccin azaune kanta na lilo.

KINASON MAGANA DANI M SHAKUR??? CLICK ON THIS LINK AND CHAT ME UP
wa.me/+2347012181461
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI💫

✍🏻M SHAKUR

JOIN INTIMACY CLASS TODAY WITH JUST 5k MY PEOPLE LEMME TEACH YOU YANDA AKE HAVING AMAZING LOVE MAKING DA YALLABAI! YANDA AKE ENJOYING SEX! YANDA ZAKI TASHI KANSA KIKUMA KWANTAR MAI DA HANKALI.
YANDA ZAKI KWANKWANCE KAN MEGIDA DA MAGANAN BANZA🔥

I AM THE BEST IDAN DAI HARKAN KARATUN NAN NE A HAUSANCE😎

Kimin magana a watsapp +2347012181461

EPISODE4️⃣

She just wished all this ayyukan wahalan da suffering da yarinyarta yar karama keyi just to take care of her itane keyi mutane bazasu gane rahama ne Allah yamaka lafiya sannan yabaka karfin nema ba gashi tana neman wannan karfin ita tafita tayo aiki ta kula da diyarta daya tak a duniya tarasa, Rasheeda ce zuwa ayyukan shara da wanke bayuka, da wanke wanke just to get paid suci abinci ga school duk ita kadai dan yanzu ma suna hutun school, yarinyarta batasan menene dadin rayuwa ba tunda ta taso sai wahala, Rashida doesn’t deserve to be born like this, ta zaman ma yarta bakin tabo arayuwanta waye zai taba auren Rashida yanzu? Ko anzo ma gulman yan anguwan nan koransu suke, babu kalan sherin da ba’a musu, kowace budurwa irin Rashida nada kawaye ita batadashi kota fara kawance iyayen yaran zasu raba abotan sabida ansan diyar mai HIv ce, yar fasika ne gantalalliya dan haka babu iyayen dakeson yaransu suyi mu’amala da yarta, hawaye masu dumi ne suka gangaro daga idanunta dasauri takai hannunta ta share fuskan tass tareda sauke ijiyan zuciya ahankali tace “Allah na yarda ka kasheni da ciwon nan, Kama karomin cuta daban daban duk na yarda, amman Ya Allah kabama diyata farin ciki arayuwanta, Ya Allah ka kawomata karshen wahalan nan, Ya Allah idan mutuwata zai zamto abinda zaisa Rashidana tadena aikin wahalhalun nan just to take care of me Ya Allah ka dauki raina dudda banson na barta, Ya Allah spare my daughter this harsh way of living and take me instead” tasake share hawayen dasuka zubomata sai kawai tadaura kasan rigan atampanta kan fuskanta tai shiru takai 2min ahaka sannan ta mike taje inda take tallabota tayi tace “Raudah oya muje ki kwanta” ina batamasan anayiba baccin yayi nisa gajiya kuma kesata baccin kaman tamutun nan, kamata Mama tasakeyi tace “tashi muje kinji Rish-rish din Mama” Mama tai maganan tana dagata da kyar ina bamata iya tafiya kaman matatta, kakkamata Mama tayi tasata ajikinta tana tafiya da ita ahankali tanajan kafa kaman irin wacce tasha giya tai tatil din nan, uwar dakin babu komi banda wata yar katifa datake a gyare akasa sai kuma manyan ganamasgo guda biyu na kaya sai dan rio na kayan kwalliya da wasu kodaddun hodon makeup da gorunan turaren humra suke ciki saikuma wata benci haka da littafai ne cike na school akai saikuma lab coat da aka makala a nail na bango jikin aljihun an rubuta Dr Rash ajiki Mama ta kwantar da ita ahankali.

Karfe 4:30 daidai tabude idanunta adduan tashi daga bacci tayi sannan takalli Mama wacce

taganta kan dadduma idan da sabo ta saba agurguje ta tashi waje taje tahura wuta tadaura ruwan wanka sannan tashare tsakar gidan taje ta wanko bayi ta watsa ruwan sanyi ita tafito tai alwala tazo ruwan yayi zafi tahadama Mama a bucket tadawo daki dan kaita bayin dan kafafunta na bala'in damunta tace "Mama muje kiyi wanka" tana rike da Mama har bayi Mama tace "karki jirani jeki salla" batai musu ba salla taje tayi sannan tafito ta daura tuwo a wuta ta kwashe kayan da Mama tasa sharp sharp ta wanke ta shanya tasake wucewa hanyar bayi tadawo da Mama dakin dahar ta gyara tafita waje takarasa tuwo tai miya tazuba komi a kula takawo daki sannan ta shirya cikin wani dogon rigan abaya baki wanda stones din duk sun ciccire tadau gyalen zata yana kenan ta tuna jiya saitahau dariya Mama dake shafa mai tace "ke lafiyanki kike dariya ke kadai?" Dasauri tajuyo ta taho wajen Mama tace "Mama wani dan gayun mutumi nasa a bola na zuzzubamai shara bakiga yanda yake makyarkyata ba kaman da zinare aka yishi ba kasa ba" yanda take murmushi tana dariya yasa Mama tace "wa kikasa a bola Doctor?" Dan tsagaita murmushin tayi tabama Mama labari kunnenta Mama taja tace "Rauda wai mesa bakiji ne inda sun kasheki ke fa dakike musu rashin kunya ina kikeso nasa raina why mesa you are always putting yourself in trouble ne eh? Mesa bakiji wai kin dauka wani karfi gareki wai sabida wani baitaba chasaki ba ko" kaman zatai kuka tace "Mama yakuri to kisaki kunnena" sakejan kunnenta Mama tayi dudda bada karfi sosai ba tace "saina cireshi duka, wai mesa bakiji eh? Why wat if wani abu yasameki?" Ganin yanda takeyi da fuska kaman zatai kuka alamun jan kunnen namata zafi yasa Mama tasaki kunnen ahankali saikuma takama kafadanta cikeda damuwa sosai tace "Doctor kinason duk idan kin fita yanzu hankalina yadena kwanciya ne?" Dasauri ta girgizakai, ahankali Mama tace "to yimin alkawari u will not put kanki in any trouble again" murmushi tayi tace "I promise Mama bazan karaba" ijiyan zuciya kawai Mama tasauke dan tasan is impossible cus Rashida and trouble are besties, tashi tayi tawuce takarasa shiryawa ta yana gyalen akanshi ta kwashi uniforms nata tasa ajakan ta sannan tazauna tahada zanen tasaka musu frames Mama sai kallonta take kawai saida tagama tass sanan tazo kusada Mama lokacin 7 daidai tace "Mama maganin safe" tadauko magani bama Mama maganin tayi sannan tacire yar wayanta daga chaji tadauki earpiece dinta tace "Mama bari inje" cikin kudin data kawo jiya Mama tazare 1k tace "ga wannan kihau abin hawa kidena tafiya da kafa hotel din nan da nisa" dasauri ta girgiza kai tace "Mama ki ijiye duk nazuwa asibiti ne next week ni dakafata zan taka ai ba nisa ko ciwon kai kikaji ki kirani zanbar kome nakeyi na dawo zanyi aiki a hotel har karfe daya biyu yau ba airport zandaiga alert, sai karfe 4 ina wajen Maman miwa bye Mama na" dasauri Mama tace "to baxaki daure ko Lipton kisha ba tunda baki iyacin abinci dasafe" dukowa tayi ta rungume Mama tace "Mama zanyi latti ne nakai zansha a hotel din ai ana bamu coffee da biscuit bye Mama kinji" ta shafa fuskan Mama tana kallonta saikuma ta manna ma Mama kiss a goshi tace "Mama kinyi kyau wlh atampan nan zaki bani ita" dan maketa kadan Mama tayi tace "ba Dr yace kidena min irin abubuwan nan ba saina shafamiki ciwo" haderai Rashida tayi sosai tai sauri zata tashi hakan yasa Mama tarike mata hannu tace "zo to fushi kikayi banso kibar gida da fushi yakuri bazan kara miki maganan ba" hawaye idanunta suka tara saikuma tahadiye hawayen saikawai ta rungume Mama tsamtsam kaman yar yarinya tace "Mama ko duka ciwon duniya kikedashi ni zan fiso su dawo kaina ke naganki lafiyanki kalau, Mama kome kika dawo ko menene ajikinki you will always be Mama na nikadai, koda zan samu I don't mind ni ko mutuwa yazo nafiso mu mutu tare ma" dasauri Mama ta daki bakinta tace "bazaki mutu yanzu ba sainaga yaranki jikokina" turobaki tayi tasaki Mama

tace “Mama ni banson maganan nan I hate maza to the core bazan taba aure ba, dana auri miji irin wanda kika aura danni ba Babana bane gwara na mutu ahaka banyi aure ba, matsiyac…….” “Doctor!” Mama takirata azafaffe hakan yasa tai shiru tadauke fuska, ahankali Mama tace “karki kuskura ki zagi Babanki” kallon Mama tayi irin why are you still protecting him sai kawai tayi hanyar fita daga uwar dakan cikin sanyin murya Mama tace “he’s your father” jakanta tadauka ta goya tace “Mama he’s not my father ko sunanshi dakikasa nake amfani da dan babu yanda zanyi ba, Mama na tsani mutumin nan and I hate all men naduniya, nidai mudaina maganan banmasan maisa kikemin maganan maza ba to mezasumin? Akwai wani hanyar neman kudi daban iyaba? Mama namafi mazan karfi laaaa nama manta ban daga karfe ba yau” tajuya dasauri zata fita daga dakin Mama tace “kika daga karfen nan saina mammakeki wlh waike namiji ne yau naga bala’i a hannun yarinyar nan” dariya Rashida tayi ta tsaya daga bakin kofa tana kallon Mama tace “Mama bakiga saisa babu me kawomin raini ba sabida ansan inada karfi Mama dan Allah kibari nadaga kinji Mama 2mins” da hannu Mama ta nunata tace “wlh zanci kaniyanki, sokike ki mummurde ki koma namiji? Wannan harkan karfen wlh bazan yarda dashi ba jira nake rannan lahadi idan Lawali yazo ince yatafi dashi” dasauri Rauda tace “wlh Mama karki bayarmin da abuna da kyar nasamu mutanen garejin nan suka saidamin da abin nan dubu uku” baki Mama tabude tace “yanzu bakisa dubu uku kin sayi sutura ba sai karfe kikaje kika saya agareji tafi aiki ki dawo zaki gamu dani wlh agidan nan” dariya tayi sosai saikuma ta buga kafa tace “to kice bazaki bayarba wlh Mama kowa kikaba sai naje na karbo abuna kota katanga ne saina haura” haba Mama tarike tace “to wani daban zan bamawa ba Lawal ba sai inga idan tsafi zakiyi ki gane wana bamawa,  wuce kitafi” tace “bye Mama na, Mamana kyakkyawa mai gashi, Mama haryau gashina yaki kamo naki narasa maisa” kaman jira Mama take tace “sabida kin soma daga karfe ne saisa” dariya Rashida tayi harda kama ciki tace “laaaa Mama wlh wannan zuki tamallo ne” baki Mama tasaki tace “ni Mamanki ke karya Doctor”? Dan sosa kai tayi kaman mara gaskiya tace “uhnnn” kwapa Mama tayi tace “wuce kitafi zan gamu dake kika dawo ai anan zakizo ki sameni” nokekai tayi tana danne dariya tawuce tafita Mama itama tai murmushi ta daga murya daganan daki tace “ayi addu’a dai kafin afita daga gida Allah bada sa’a” tsayawa tayi tai addu’a sannan tabude kofa tafita abinta tana rike da frames na artwork datayi guda uku ga jaka abayanta she’s just a young lady da kana ganinta kaga strong, bright hardworking young lady, Nisan daga gidansu zuwa hotel din kusan tafiyan awa daya cur tabar gida bakwai takai hotel din by 8, Babban hadadden hotel ne shima gyare gyaran daki take da da bayika su wata wata suke biyanta 30k office na wajen da uniform nasu taje ta chanza kayanta taciro uniform din tana sawa Riga da wando ne tana kokarin saka karamin farin hijabinta wata tashigo dakin hakan yasa dasauri tajuyo hada ido sukayi da yarinyar tana ganin gashinta tace “Innalillahi Rashida kinasa attachment ne”? Dan zaro manyan idanunta  Rashida tayi dan bama tasan gashinta ya warware ba hannunta yarinyar tadaura kan gashinta bakin kirin gashi da sulbi ga tsayi sosai tace “wlh gashin kine Woww Rashida hala ku ba yan Nigeria bane” fizge gashinta Rashida tayi kaman fada tashiga parking tace “kada ki kara tabani” baki yarinyan tasaki tace “ohhh nidai bantaba ganin masifaffiya irinki ba daga na yabi gashinki Rashida sai fada” saka hijabinta tayi tace “aiki kikazo yi ko yabon gashi”? Tana maganan ta kwashi frames din tabar wajen yarinyar tabita da kallo har cikin ranta tanason tai kawance da Rashida but Rashida irin mutanen nan ne mafadata and too protective is as if batason mutane su shigo space nata because she don’t wanna get hurt oho, u can’t

complement her, u can’t say anything to her fada but batada neman tsokana, bata shiga mutane ba ruwanta da kowa itadai tazo tayi aikin datazo yi lokacin tafiya nayi ta tafi ko minti daya bata karawa.

Sosai manager ke kallon zanen saikuma ta kalli Rashida tace “anya kene kikai zanen nan kodai satowa kikayi”? Zaro manyan idanunta tayi tace “tunda nake bantaba sata arayuwana ba idan baki yarda ninayi ba bani paper da pen da color namiki exactly irinshi agabanki” murmushi manager tayi takalli abin saikuma tace “zan saya akan 10k each sannan ki dingayi kina kawomin ko guda nawa ne zan saya” bakaramin dadi Rashida tajiba dudda zanen zane ne da har 100k zaa iya saya awani waje but bata damuba 10k is huge 30k ta kirgo tabata sosai Rashida taji dadi bata taba sanin zata iya saida zanenta ba kaman fa wasa taji ana maganan sayan frames tace ta iya manager tace takawo tagani jibi anbata 30k akan guda uku anatse tace “nagode Ma Allah kara arziki” dan tabe baki matan tayi tace “tafi kifara aikin ki” wucewa tayi tafita manager ta kalli frame din tace “zan gayawa Oga 150k each nasaya wayyooo this girl is talented bata sani ba inhar Oga yasosu zance muyi ma all rooms na hotel namu nabama yarinyar tamin I will be fucking billionaire nabata 10k each ni na karbi 150k for each awajen Oga wow look at her work”.

FOLLOW ME ON TIKTOK AND CATCH UP WTH ME

https://www.tiktok.com/@mshakurr?_t=8m0Y3PbS2GD&_r=1
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

RUN TO HABISHMA GROUP NOW KUZABI SU BREZIYA DA PANTUNA DA KAYAN BACCI DAKUKE SO KUCE DAGA WAJEN M SHAKUR KUKE KUGA KALAN PRICE DAZA’A BAKU ME RAHUSA🔥🔥

JOIN NOWWWWW
https://chat.whatsapp.com/KGCjEvBSvUk3TY9ZHC2iWv

EPISODE5️⃣
Ahankali yake bude idanunshi kadan kadan sama sama yaji ance “Son” dudda idanunshi akulle but ahankali bakinshi ya furta. “Momm” shafa mai kai matan tayi ta duko ta manna mai kiss agoshi cikeda tsantsan so tace “gani nan yarona open yourself Riyad no one is gonna hurt you again” gently yake bude idanunshi kafin ahankali ya saukesu akanta gently ya yunkuro ya shige jikinta kaman dan karamin yaro yace “Mommm” bayanshi ta shafa tana murmushi tace “meya sameka what happen? Who did this to you”? Murya chan kasa yace “wasu mutane wanted to

kill me….” Kankameshi tayi sosai tace “babu wanda ya isa ya cutarmin dakai ko yadauki rayuwanka as long as ina raye, u are safe already ana investigating abun sai inda karfina yakare” takara kankameshi kaman dan karamin yaro tace “I love you Riyad kaine kadai sanyi idanuwa na”lumshe idanu yayi saikuma ya yunkuro yatashi daga jikinta yakalleta da muryanshi da bata fita sosai yace “Baba”? Kallonshi tayi saikuma ta sauke dan ijiyan zuciya tace “tashi kaje kai wanka ka shirya kafito ka gaggaisa da mutane idan zaka iya, sannan kaje kama Babanka addu’a a makwancin sa” dan runtse idanu yayi abin yamai ciwo yaso Ya sallaci mahaifinshi, fuskanshi Mom ta taba hakan yasa yabude idanunshi dasukai ja yakalleta murmushi kadan tamai tace “nasan yanda kakeson mahaifinka but he’s in a better place yanzu trust me, all abinda yake bukata awajenka is addu’a, jekai wanka za’a kawo maka kayayyakin dazakasa” gyadamata kai yayi agajiye yace “Mom please ke kikawomin banson hayaniyan kowa” tsayawa tayi ta kalleshi ahankali tace “tom zan kawo maka da kaina” dagoshi tayi yatashi tsaye ahankali yawuce bayin dake nan bedroom din, girman bayin yayi girman wani gida, wanka yayi yayi brush yadaura towel yafito yana kallon saman gadon inda tundaga kan takalmi har zuwa kan agogo an jeramai akan gadon tsaf dazai saka wasu kayan sarauta ne masu kyau sunsha aiki, anatse yake komi ya shirya cikin kayan da aka musu aikin royalty ya feffesa turare yadan juya yakallo kanshi amadubi yayi wani irin kyau na ban mamaki hulan dayasa yasake maidashi wani cikakken mutum bude kofa yayi yafito daga bedroom din wasu bayi ne ma’aikata a falon suna ganinshi suka duka dukansu. “Takawanka lafiya Yarima Riyad, taho a sannu dan kwalisa abin begen Sarauniya Maryama, barka da fitowa, Allah yakara maka lafiya, makiyinka fadawanka, duk wanda yaja dakai ya shirya yasha kasa….” Wucewa yayi fuuuu yafita danshi bayason wayan nan surutun nasu, da Munir yaci karo yana kokarin shigowa flat dinsu hakan yasa ya tsaya yahade rai kaman suna fada Munir yace “katashi, are you feeling better can you walk”? Gyadama Munir kai yayi yay gaba kawai, Munir yabishi abaya direct inda aka binne sarki yayi yana zuwa ya shiga wajen batare da an hanashi ba yayi shiruuuuu idanunshi sukai ja, almost everyday indai Mai Martaba baida wani uzuri saiya kirashi da daddare yaji yayake ina kuma yake, kullum cikin fada yakemai daya daina yawon kasashe yakan yawan cemai yanda yake gudunma gidan nan da alamu shine wanda gidan nan zai rike kuma gam, ana cewa sarakuna basu da lokacin yaransu shidai mahaifinshi nada lokacinshi, Baba ya fara koyamai business how to make 1naira yakoma billions, Baba guides him through everything, duk business dazai fara saiya kira Baba, sai Baba ya amince zai farayi, kuma bai taba takura mishi ba, hawaye yaji sun taru a idanunshi da sauri ya runtse idanun yana fuzar da iska dan baiso suma zubo but he’s deeply hurting, da ace yasan Baba zai rasu dabaiyi tafiyan nan ba, sosai yama mahaifinshi addu’a sannan yafito Munir yagani awajen da Kabeer dasu Shaibu yan uwanshi dukansu yajiki sukamai ya amsa sai kallonshi suke Kabeer yace “kasha magani kuwa you still look sick? Ko zaka koma ka kwanta ne”? Gyadamai kai yayi ahankali yace “nasha, I’m fine thank you” dannewa Kabeer yayi ganin yanda yakemai magana kaman alfarma yakemai dayake amsashi yadai daure yace “to mutafi fada” atare dukansu suka wuce fada, sauran yayyinsa da yan uwansa natamai hira da uhm a’a kawai yake amsasu cus gashinan ne kawai, gaida mutane sukayi sai yima Riyad gaisuwa ake ana kiran sunanshi shi baimasan ya akayi akasanshi hakaba dan baicika zama ba, su Waziri dai duk suna kallon komi, kowa yazo saiyamai gaisuwa amai yajiki, yanda ma ake kallonshi sai abin yasa yaji sabon zazzabi na nema ya lullubeshi.

Mom nazaune afalonta tana jan charbi ita dawasu kawayenta wanda suke mata Sarkin daga wasu garin dasuka kawo mata gaisuwa aka shigo flat din Matan Waziri ne da babban diyarta Haleema da ake kira da Lims, tana sanye da doguwan riga abaya black ta yana gyalen akanta, tanada tsayi da dan jiki kadan duka duka bazata wuce 24, 25 ba, tana shiga dasauri tawuce wajen Mom kafinma Mamanta tai gaisuwa tace “Mom ina kwana” takalli sauran matan wajen cikeda girmamawa tace “ina Kwanan ku” amsawa sukayi Mom tamata murmushi tace “Halima ba kina school ba yaushe kika dawo”? Mahaifiyarta tace “nima ganinta nayi agida da safen nan ta iso daga London wlh na aika driver yaje yakawota tunda taji rasuwan Mai Martaba hankalinta yakasa kwanciya” sosai Mom ke kallonta akunyace Haleema ta sunnar dakai Mom tace “school fa idan kikai missing exam ko test fa” Maman ta tace “project ma fa takeyi this month zasu gama komi da komi” babu wasa kan muryan Mom tace “kibi first available flight ki koma school gobe kinajina” gyadama Mom kai tayi ahankali tace “to Mom” Mom bata sake cewa komiba tacigaba da magana da manya, ahankali Haleema kebin dakin da kallo gabanta na faduwa addu’a take Allah yasa suhadu ta ganshi, Allah yakawoshi side din nan dudda tasan ba lallai yadawo ba barinma yaji da baki adakin amman tasan inhar yana gari yafi zama wajen Mom da bangarensu na samari.
Kallonta Mamanta tayi tace “tashi kije wajen su Batul mana” juyowa Mom tayi takalleta tace “tashi kije wajen yan uwanki” batai musu ba tashi tayi tawuce tafita Matan Madaki tabita da kallo tace “yarinyar akwai natsuwa ga kunya ga kawaici ta dace da Riyad sosai yanda shima baida maganan nan” wani kalan dadi Matan Waziri taji Mom tai dan murmushi batace komiba.

Ahankali take tafiya ita kadai tana danna wayanta kamshin turaren dataji yasa ta dago kanta dasauri Riyad tahango yafito daga fada yana shigowa nan compound din Mom wlh kusan duka yaran sarki tasansu da yaran yan uwa dan afadan nan aka haifeta anan ta girma bata taba ganin yaro mai kyau da farin jini da aji irin Riyad ba kap gidan nan babu wanda yakaishi kyau, ga tsayi ga gayu ga jidakai ga miskilanci ga kudi kudinshi na kanshi bawai kudin Baban su ba dan babu wanda yakaishi kudi a yaran sarki, gashi Mai Martaba na sonshi, ga kakanshi na bangaren Mom Attorney General yafi kowa tsatso mai kyau da gata ayaran sarki.

Faduwa gabanta yayi sosai amman tadaure ta tsaya awajen jikinta har bari bari yake, tahowa yayi wajen batare daya kalle inda takeba zai wuce dasauri tace “Yarima Riyad!” Tsayawa Riyad yayi chak batare daya juyoba dasaurinta Halima taje ta gabanshi ta tsaya adan kunyace tace “ina yini ya hakuri?” Dan kallonta yayi trying to remember waye ita, shifa wasu kannin nashima ba saninsu yagamayi ba dan baya shiga lamarin gidan nan baison komi game da sarautan, dauke kanshi yayi ganin yanda take murmushi tana kallonshi, kaman ance dole yayi magana yace “who are you”? Wow the way he talks is super adorable, da kyar ta iya controlling zuciyanta dake neman fitowa ta danne kome takeji tace “Haleema” dan kallonta yayi irin kallon okay but still baigane ta ba and he doesn’t care din nan yajuya zai wuce dasauri tace “Ya Riyad sabida kai nazo gobe zan koma school” dan tsayawa yayi wannan karan yajuyo kalleta da kyau shifa har yanzu bai santaba and sabida shi tazo? Akan wani dalili? Are they related in anyway? Infact baida karfin bude baki ma yayi all this questions hakan yasa yadan tabe baki yace “thanks” kawai yawuce ya shiga flat din Mom……

Jin akwai baki abangaren Mom yasa yajuya yagazaya ta baya yashigo gidan yaje ya kwanta.
**

Yana zaune adakinshi dashi da Munir har yanzu bai gamajin sauki ba yana sanye dawani 3quater da singlet wayanshi yahau ringing kallon wayan yayi ganin Mom yasa yadauki wayan kai tsaye tace “kazo dakina ina son ganinka” ahankali yace “okay Mom” tashi yayi ahankali Munir dake taba wayanshi yace “ina zaka?” Slippers yashiga sawa yace “Moomm” yadauki wani farin t-shirt yasaka kawai yawuce Munir daya gane abinda yake nufi wato Mom nakiranshi hakan yasa yacigaba da abinda yakeyi ahankali yabude dakin Mom tana zaune kan couch din dake dakinta ganinshi yasa tanunamai gefenta tace “taho nan” shigowa yayi ya maida kofan dakin yarufe yataho wajen kujeran zama yayi saikuma ya kwanto yayi filo da cinyanta he’s really feeling mutuwan mahaifinshi so duk walwalanshi bayanan, hannunta Mom tadaura saman kanshi ta shafa tai shiru kafin tasauke ijiyan zuciya tace “kasha magani kuwa? Dr zai zo anjima” ahankali yace “nasha” dan ijiyan zuciya tasauke tace “da banson namaka maganan nan yanzu cus nasan kanajin mutuwan Babanka, I know how much you love mahaifinku Riyad but I have to dan kowace matan sarki maganan da datake ma danta maza kenan, nima dole nama nawa” dan dago idanunshi yayi ya kalli Maman nashi baice komiba, ahankali tace “inaso kai aure Riyad!” dawani irin sauri Riyad yatashi zaune daga jikin ya kalleta yama kasa magana cus maganan yazo mishi ne bagatatan, Mom dake kallonshi itama looking damn serious tace “and bakowace kalan yarinya nakeso ka auromin ba Riyad, inaso ka auri yarinyar da zuciyana ta aminta da ita yarinyar da nice na zabeta, all yammatan zamanin nan yanzu burinsu is suyi aure su raba yaro da mahaifiyarshi I will never allow you marry such girls, I have a girl a mind dina gaskiya” haderai yayi kana ganin fuskanshi kasan bama yason maganan dasauri yace “Mom aure!”? Wani mugun kallo tamai tace “kaga Riyad banson shirme don’t even start all abinda kakeso kace, I supported you duk yawace yawacen dakake kana touring round the world bantaba hanaka ba dan nasan it’s your hubby, bantaba takuraka ba dudda normally normally ba tun yau yakamata kai auren ba, but yanzu lokaci yayi it’s an order you have to settle down, aure zakayi and i have a girl danakeso ka aura diyar Waziri Haleematu, ita nakeso ka aura!” Wani kalan tashi yayi dasauri yamike tsaye yana kallon Mamanshi da babu wasa akan fuskanta itama tabishi da kallo tazubamai idanu rass aka tace “kaine the most successful child acikin yaran sarki, you’ve archived alot Riyad at a very young age, ga ilimi kwali daban daban gareka, ga businesses da companies daka bude, ga natsuwa ga kamala ga kwarjini, naji kishen kishen dama mai Babban daki kaine zabinta sabida yanda mahaifinku ke sonka, Waziri shima nasan kodan yanda diyarshi ke sonka kuma yana mata kwadayinka kaizai dangwalamawa, to yaji maganan kuma kanason auren diyarshi komi yazo cikin sauki idan yana bangaren mu zai mana aikin yima sauran manyan fada maganan a zabeka, instead of su Kabir yan uwanka ko kannen babbanku dake neman kujeran sarautan, gwara kai dana kaikafi kowa chanchanta and bazan hutaba saina maidakai sarki, ai tsoron kada ka zama sarki yasa daga shigowanka garin suna neman halakamin kai amman Allah bai basu iko ba, kuma naji dadin abinda yafaru hakan yanunama jama’a cewa an tsaneka ana tsoron kada ka zama sarki saisa har anfara yunkurin kasheka, saisa saida na tabbatar kowa yasan abinda yasameka”.

WANNA TALK TO NI M SHAKUR DIRECTLY?? KIMIN MAGANA A WATSAPP
+2347012181461
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

KINSAN YANDA AKE JIYAR DA MIJI DADI? KINSAN YANDA AKE SA ME GIDA KUKA AGADO? KINSAN SIRRIN SARRAFA TANTAKWASHIN DADI? KIN IYA HATSABIBIN KUKA? MAKIRIN KUKA? SHEDANIN KUKA DA AKEMA MIJI? KIN IYA STYLES? KIN IYA KISSA???

JOIN INTIMACY CLASS DINA WITH JUST 5K KI KOYA🔥

GROUP DIN TSAWON SHEKARA DAYA NE KIKA BIYA 5K BAKI KARA BIYAN WANI KUDI SAI BAYAN 1YEAR JUST TODAY AND BE A BADDIE FOR OGA🙈

CHAT ME UP DON SHIGA
+2347012181461

EPISODE6️⃣
Wallahi kanshi ma sarawa yafarayi jin maganganun da Mom kemai, first of all duk wani abun na sarautan su bayaso saisama baya iya zama agarin, baison hayaniya baison how they do things cus is always fighting, makirci and politics, and baijin tunda ya girma yatabayin cikakken 2months like good 60days agidan ba bini bini yabar country, lokutan salla ne yasan dole yake dawowa sabida yanda Baba ya maida abin mandatory yanason duka yaranshi to be home sabida hawan salla and other activities na al'adu, shi mutum ne da baisan mulki he prefer business nashi, he derive joy a business, it gives him purpose, for aure kuma dudda yasan culture nasu ne amaka aure abaka mata but shi kwata kawata baitaba sanin Mom zatamai hakaba cus Mom is highly educated and expose, itama bata cika biyema culture ba saisa ma take barinshi to live his dream life, ko kadan bai shirya aure ba cus bayason commitment for now, his plan is nan da 2yrs zaiyi aure yanzu kawai aure baya lissafinsa, dukawa yayi ahankali gaban Mom yadafa kafanta kaman zaiyi kuka yace "Mommmmm" ahankali itama Mom tana kallonshi tace "Riyaddddd! You don't have to say abinda zaka fadi kasan nasanka sama da kowa aduniya ko?" Gyadamata Kai yayi Mom tace "I know how you despise sarauta, mulki infact bakamasan komi akaiba, I know for auren zakace baka shirya ba bakasan damuwan mace da sauransu" sai kawai takai hannuwanta tai cupping face nashi cikin tattausan lafazi tace "dama akwai abinda zan taba so aduniyan nan dabaza ka iyamin ba Riyad"? Ahankali Mom tace "I thought nine number 1 dinka like you always say"? Dasauri cikin raunin murya Riyad yace "Mom u are my number 1 kema kin sani" kai tsaye Mom tace "inhar nine number one din

naka then karka karamin gardama kan maganan nan it's an order allow me to do everything am I clear?" Yadade yana kallonta yanda take kallonshi babu wasa kan idanunta yasa ya sauke kanshi kasa alamun dai baiso but baice komiba, baya iyama Mahaifiyarshi gardama, cikin fushi Mom tace "kamin shiru? Ban isa dakai bane ko ban isa nace maka haka nakeso kayi kayiba"? Tai maganan tana shaking leg in anger, abu yahadiye awuyanshi har saida taga motsin adam apple nashi asanyaye yace "okay" tsayarda shaking leg din tayi tai murmushi sai kawai ta matso ta mannamai peck agoshi tace "I wish kowacce uwa zata sami d'a mai mata biyayya kaman Riyad dina data zama very very lucky, Allah maka albarka kaji, Haleema is a good girl tana matukar sonka tun tana yar yarinya, she will keep my son happy I'm sure of that, so karka damu, zancen sarauta kuma I will teach you everything and you will do well kaji"? Gyadamata kai yayi zuciyanshi duk ba dadi duka duka kwanan Babanshi nawa da rasuwa but kowa is after kujeranshi, look at matayensu kaman ba mazajensu ne suka rasu ba dukansu kokarin daura yaransu kan Sarautar suke sunma manta da rasuwan shima yanzu yazama sarkin one day haka matarshi zatayi kenan itama yana mutuwa all focus dinta will be yanda danta zai gajeshi bamatada lokacin yimai addu'a tashi kawai yayi yajuya yayi kofa.

Mom tabishi da kallo ranta fess, dolema Riyad dinta yadinga intimidating kowa, yafi duka yaran sarki kyau ga kwarjini ga haiba ga natsuwa, ga jan aji, ga kudi, ga rashin magana, ga rashin shiga mutane, gashi baida kallon mata shi kadai keda qualities na sarki and bazata hutaba saita maidashi sarki wannan alkawari ne!.

Dakinshi yashiga Munir dake danna laptop yabishi da kallo ganin yanda mood dinshi ya chanza tashi daya,   Wucewa yayi yafada gado yakife cikinshi tareda lumshe idanu Munir baicemai komiba yacigaba da abinda yakeyi abinshi.

Yana fita Mom ta daga wayanta takira matan Waziri da ake kira da Mariya ringing daya ta daga wayan tace "ranki shi dade Uwardakina, Allah yaja zamaninki Umman Riyad" dan murmushi Mom tayi kafin cikeda isa da jiji dakai tace "dole gobe Haleematu zata koma makaranta ne"? Dasauri Mariya tace "ai Uwardakina ko makarantan kikace karta kara zuwa saita zauna" jinjina kai Mom tayi tace "tom inaga bazata tafi goben ba dan zan turo Riyad yazo ya ganta inaso nahada su aure inyaso bayan yaganta zata iya tafiya" wani ihu Mariya tayi cikin waya saikuma ta zube kaman tana gabanta tace "nagode nagode Uwardakina da wannan karamci naki, kidubi kowa na gidan nan amman kuka zabinma Yarima Riyad Haleematu nagode, namiki alkawari bazaki taba samin matsala damu ba, I will forever be loyal to you, Haleema zata bautamiki Uwardakina, kuma da yardan Allah kujeran sarautan nan ta Yarima Riyad ce ai naji jita jita, da yardan Allah shine magajin sarki" dan murmushi Mom tayi tace "Waziri ya shigo yakirani" tana maganan ta katse waya wani ihu Mariya tayi tamike da gudunta tafice zuwa dakin  Haleematu kai tsaye tabude kofan yarinyar na zaune sanye da rigan bacci tana kokarin hada kaya Maman kawai ta dagata tana juyawa tana rawa abinma saiyasa Haleematun dariya tace "Mommy menene kike murna haka"? Cikeda jin dadi tace "yanzun nan Sarauniya Maryama takirani tace tanason hada aurenki da Yarima Riyad gobe ma zata aikoshi gidan nan" wani kalan zaro idanu

Haleema tayi she can’t believe abinda taji tun tana yar yarinya takeson Yarima Riyad yahadu ne over wlh, lips nata rawa suka fara farinciki yahanata magana tace “Mommy mekikace? Yarima Riyad mene? Dan Allah maimaita”?Kyalkyacewa da dariya Mama tayi tace “dalla cewa nayi za’a aura miki Riyad zaki zama matan sarki dan ina mai tabbatar miki shi za’a bawa Sarautan” ihuuuu tayi tareda wani kalan tsalle ta rungume Mamanta sai kawai tahau tsalle sosai lekowa dakin Waziri da shigowan shi kenan yayi ganinsu yayi murmushi waya na kunnenshi Mama zatamai magana yadaga hannu yace “inajinki ranki shi dade” wucewa falo yayi yazauna Mama da Haleema suka biyoshi a speaker yasaka wayan dashi da Mom ke magana suna shirya komi kaman ba mutuwa aka musu ba, planning auren da yanda zasu sami kujeran suke hankali kwance.
**

Wuraren 10 yafito daga dakinshi yana sanye cikin wani farin yadi da akamai dinkin jumper yamai kyau sosai sai kamshi yake zubawa kaman zaije gasan turare, binshi da kallo Mom tayi tana murmushi tace “Son katashi? Munir yashigo yakai sau uku nacemai bai isa yatasheka ba, bayan kunyi sallan asuba tare a mosque” karasowa yayi yazo kusadab da ita yazauna ahankali yace “morning Mom” as usual pecking nashi tayi a goshi tareda shafa kumatunshi tace “morning Riyad, yaya jikin? Zakai breakfast yanzu ne”? Girgiza mata kai yayi alamun no, dasauri tace “to maza je Gwaggon ku ta aiko dazu akiraka kadawo saikai breakfast kafin kafita fada ko”? Dan gyadamata kai yayi yatashi ahankali yayi kofa haryasa hannu zai bude kofan tace “idan tamaka maganan auren Haleema kai naam” dasauri yajuyo da kanshi ya kalli Mom dauke kai tayi kafinma yamata wani maganan, dan jim yayi sannan yabude kofa yafita ma’aikata fada sun cika wajen yawanci Mom bata barinsu falo so anan waje suke yashe kaman kaya, gaishe gaishe da kirari sukahau mai ya wuce abinshi ko kadan baison zuwa wajen Gwaggo shi kadai hakan yasa yaciro wayanshi daga aljihu dailing number Munir yayi ringing daya yadaga yace “kana’ina”? Daga dayan bangaren yace “ganinan daure da towel wanka zan shiga” dan yatsine fuska yayi yace “be fast to” ya katse wayan baiso ya koma ciki dan baiso Mom tasan baijeba kuma baison yayita tsayawa awajen hakan yasa yawuce flat din su Munir wanda da dan tafiya sai gaidashi ake bai amsa kowa har gaban flat din tsayawa yayi jimmm awajen sai chan yasa hannu yabude kofan da sallama ahankali hada idanu yayi dawata mata dake zaune a falon sanye da hijab da charbi a hannunta kaganta kaman ita tai kakinshi ta tofar sunyi kama sosai, itama tanada haske kaman shi, sauke kanshi yayi kasa da sauri sannan ahankali yashiga ciki tareda maida kofan yarufe yama kasa magana, tadade tana kallonshi sannan tasauke kanta kasa tace “Munir nasama kaje ka sameshi” gyadamata kai yayi sai chan kaman me tsoron magana yace “ina kwana Mami” batare data kalleshi ba tace “yajikinka dafatan basu maka komi ba”? Dan dago kanshi yayi yakalleta ganin kanta akasa yasa shima ya maida kanshi akasa yace “I’m fine” daidai lokacin Munir yaleko daga sama daure da towel yace “ina fitowa daga bayi naji kamshin turarenka wlh daukomana breakfast kataho dashi” mugun kallo yamai saikuma kawai yawuce dinning din yazauna yana bude warmers din saman table din,  ganin shayi dayaji kayan kamshi mai zafi dasauri ya zuba a cup ya debi waina da pepper soup yadade rabon dayaci traditional food kawai yahauci bini bini Mami na dago kanta tana kallonshi dudda yabama falon baya, sosai yakecin abincin dan yanada ci yana cikin ci wayanshi yahau ringing ganin Mom yasa

yahadiye wainan bakinshi da sauri yakai wayan kunnenshi kafin yayi magana cikin kakkausan murya strictly Mom tace “kana ina Riyad?” Kasa magana yayi yay shiru cikin masifa sosai Mom tace “okay sabida na barka tareda Munir shine yanzu gidansu kake zuwa kasan nida matan nan bamayin juna but you keep going there kana ganin gidan nan kowani yaro najin maganan uwarsa ni ban isa kaji nawaba ko ai shikenan kayi duk yanda kakeso…..” “Mommm!” dip ta katse wayan dasauri yatashi yajuyo sauke kanshi kasa yayi cikeda girmamawa yace “Mami bari naje in Munir yafito yasameni awajen Gwaggo” ahankali Mami tace “okay” kofa yayi dasauri yabude yafita tabishi da kallo sai kawai ta sauke ijiyan zuciya, wajen Gwaggo yawuce, Babban flat ne uwa gari guda, ga hayaniya ana shiga da fita masu aiki sai gaidashi ake kaman anga sarki amman ko kallon mutum daya baiyiba harya shiga dankareren falon Gwaggo, dudda dakin yacika da mutane yana shiga Mai Babban daki ta sallami kowa falon yarage daga ita sai shi yawuce wajenta yazauna yayi shiru, fuskanshi Gwaggo ta taba sannan takama hannunshi tabi da kallo tana dube dube tace “yaro jiki uwa na baturai kai kenan baka isa kaga kazanta ba” murmushi yayi ya fizge hannunshi yace “Gwaggo ni na warke kidena dubamin jiki dan Allah” tsuki tayi tareda hankadeshi tace “kaga shashasha” Hararanshi tayi tace “ni shiga dakina ka dauko huran dana dama maka daga babanka sai kai kap cikin jikokina keson furana” jikinta yayi sanyi shima haka sai yayi shiru ganin yanda yayi yasa da sauri tai murmushi tace “bance kamin fuskan mara lafiya ba, Allah shiya bani babanku kuma shiya amsa Alhamdulillah d’ana yayi abubuwan alkhairi da dama aduniya yayi shukoki daban daban, ya gina makarantu, rijiyoyi, gonaki dan haka banda nadama Allah ubangiji yakai haske kanarinsa jeka dauko” tashi yayi ahankali yadauko kwaryan fura yazo yazauna yafarasha anatse tana kallonshi harga Allah itama zatazo Riyad yazama sarki cus yarone mai tausayi mara hayaniya ga kwarjini ga biyayya sannan ga kwazo, baida sa ido, shine yaro na farko kap yaran sarki daya fara neman nashi da kanshi, tun ana gulma ana cecekuce but marigayi yace abarshi yayi abinda yakeso dudda kalan kudi dayake dashi baitaba raina wani ko yadingaji yafi kowaba gashi da tausayi ya tsani yaga wani na fushi ko kunci sanadiyanshi dan haka itama Riyad ne zabinta daman tariga ta jefamai kuri’a. Ahankali tace “zabinka ne diyar Waziri ko zabin Mamanka Maryama dan nasanta da tsinannen taurinkai, dason saka kabi ra’ayinta sabida taba Allah ya yoka me biyayya, kaika zabi Haleematu”? Abu yaji ya tsayamai awuya but ya daure ya gyadama Gwaggo kai batare dayayi magana ba, Gwaggo tace “ai shikenan za’ai magana idan anyi bakwai na babanka muji, zanma Baffan ka Muji magana nama kirashi daman” daidai nan Munir yashigo yana zama akai sallama Mujitapha yashigo yana sanye da manyan kaya daya fito da katon teban daya ijiye sai kyalli shaddan jikinshi yake kana ganinshi kasan yasha kudi ya koshi waje ya samu ya zauna hakan yasa daga Munir har Riyad suka gaidashi atare. “Ina kwana Baffa” binsu yayi da kallo shikebin mahaifinsu yanason yaran wanshi baida matsala dasu, yanason ya gaji sarautan but then again idan baisamu ba no big deal idan any of yaran wanshi suka samu, adai dauko wani sarki ne daga cousins nasu da sauransu shine bazai yarda ba, anatse yace “kai yajiki? Kasami lafiya?” Gyadamai kai Riyad yayi Baffa yace “har yanzu ana kan investigation koma su waye sukai kokarin kasheka za’a kamasu, so don’t worry, it’s good zakai aure koda bakai maganan ba ma yana cikin plan dina nace kafito da mata you need to settle down shi lokaci baya jiran kowa mutuwa ake kullum” Munir ya kalla daketa sunnar dakai yace “kaikuma fa yaushe zaka fito da taka matar?” Dasauri Munir yadago kanshi saikuma ya nuna kanshi foolishly yace “Baffa ni” akufule Baffa yamai dakuwa yace “a’a ni” Gwaggo ta zubamai rankwashi tace “dan kaniyanka

kaima kafito da mata akace" kabar da hannun Gwaggo yayi yana turo baki yakalli Baffa yace "toh Baffa zan fara nema daga yanzu" gyadamai kai Baffa yayi yace "kutashi kuje toh lemme speak to Mama" tashi sukayi suka fice daga dakin.
Direct dakin Mom yayi yana bude kofa Mom tace "get out Riyad" gaban kofan ya tsaya yace "sorry Mommy please Munir naje kirafa yarakani wajen Hajiya"

Cikin fushi Mom tace "tell me Riyad akwai abinda kataba so daban maka ba? You showed me duk cikin yan uwanka Munir kakeso dudda ban shiri da mahaifiyarsa but nabarka dashi but na gayamaka kadena zuwa side dinsu banso banso yare nake maka daka kasa fahimtata eh?" Ahankali yafara tafiya yakai inda take sai kawai ya rungumeta ashagwabe yace "I am sorry Mommyyyy bazan karaba kinga banda lafiya karki fushi dani please am missing Dad already abin zaimin yawa" shiruu tayi saikuma ahankali tace "okay nahakura but baka ba ita that woman is the reason har Babanku ya rasu baya shiri dani she come between ni da shi, allow me to plan your wedding and coronation in peace kaji" sakinta yayi sai kawai ya daura kanshi kan cinyanta ahankali yace "Mom kimin auren na yarda but please Mommy banson nazama sarki dan Allah I am too young to be Sarki, Mom I want to tour round the world with my wife in peace" cikeda fada tace "kaje sama da 58 countries wani tour round the world ne yarage bakayi ba? Is time kayi taking responsibility naka Riyad, you are royalty Riyad, kai Royal blood ne ba normal samari out there ba, duk wanda aka haifa a royal family akwai high possibility zai iya zama king so accept your calling, and Babana zai turo bodyguards dazasu dinga binka anywhere and everything" dasauri yatashi yace "Mom banso wlh banso" wani kalan kallo tamai tace "did you even know su waye da waye ke kokarin kashe ka?" Kallonta yayi yace "suwaye?" Tana kallonshi tace "I don't know but my gut is telling me Yayanku from the way yake eye service dan he's everywhere, da yarinyar nan bata cecekaba I don't know what would've happened" dan ijiyan zuciya Mom tasauke cike da damuwa tace "kullum bana baccin dare sabida tunanin wasu out there are trying to kill my son" dan lumshe idanu Riyad yayi ahankali yace "Mom lemme see the footage" iPad dake gefenta agadon tadauka ta bashi daidai lokacin akai sallama yar aiki ta gayamata tai baki tashi tayi tawuce tafita shikuma ya kwanta ahankali kan gadon tareda playing footage din da aka samo daga airport din yana kallo kusan footage biyar ne daban daban tun na shigowan shi arrival hall dana elevator saina bayin wanda shine na ukun, tsare cleaner yarinyar da ido yayi, a lokacin da abin yafaru bai wani kalleta ba dan yana cikin tashin hankali sai yanzu yake kallonta on this footage dudda is not that clear video karkar dinnan but yanda ta turashi cikin sharan yakala da yanda tarufe da how she handled everything ahankali yace "who is this feisty gurl"? The way takebin music yake kallo, he was actually watching the footage to see kozai gane criminals din but yana fara kallo attention nashi kawai yadawo kan cleaner, har footage data kaishi wajen dumping shara yakala da yanda take tafiya sai kawai yayi pursing video tareda zooming face nata yace "who are you? You saved my life."
CHAT ME UP DIRECTLY BY CLICKING ON THIS LINK

wa.me/+2347012181461
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

HAPPY JUMMA'AT GIFT 🎁

EPISODE7️⃣

Zaune suke dukansu afada, dan kowa yanzu is at home babu wani maganan zuwa aiki ko wani abu zaman makoki suke, yawanci Kabir ke attending, Riyad na zaune inda yake hardly yake magana, wayanshi ne yahau ringing ganin Mom yasa yadauka yakai wayan kunne batare dayayi magana ba, Mom tace "come nayi arranging private outing dakai da Munir da 2 security personnel da Doddo (Baban Mom Attorney General na Nigeria) ya aiko maka dashi daga Abuja kuzo kuje kaga Haleema gobe zata wuce school" jiyayi kawai ranshi yabaci amman yadaure ahankali yace "okay" yazare wayan daga kunne, kallon yayinshi yayi yace "Mom nakirana bari naje" gyadamai kai sukayi banda Kabeer dako kallonshi baiyiba, tashi yayi a tsanake yana gyara zaman milk jumper rigan dake jikinshi nawani attajirin yadi, fadawa sukahaumai kirari. "Takawanka lafiya Babban mutum! Yariman dashi kadai aka haifa agarin Riyad mai martaba yabashi suna Riyad, dan kwalisan zakaran da ya riga yayi cha….." wucewa yayi dasauri yafice dan baiso yawuce side na Mom a falo yasameta ita kadai tai murmushi ta taso dasauri tana gyaramai gaban wuyan riganshi tace "Masha Allah, yarona akwai kyau wlh, bama saika chanza kaya ba" ashagwabe kaman zaiyi kuka yace "Mommmm" dan hararanshi tayi tace "shagwabanka will not work nabiye maka u will never get married ko Doddo yayi na'am da decision din" ahankali yarike hannun Mom din kaman dan yaro yace "but Mom I don't even know the girl balle na sota" dan shiru tayi tana kallon yanda yake mata wanda halinshi ne duk girmanshi idan bayason abu haka yake mata shagwaba at this point so take ta lallabashi dan batason tasake fada da yaronta datakeso sama da komi aduniya cikeda so tace "Son you are from royal family yawanci haka ake aure, first wife din Baban ka Maman su Kabeer da 2second wife dinsa Maman su Munir duk auren hadine baya sonsu, mai Babban daki ta zabamai su ya aura dan bayaja da maganan mahaifiyarsa, daga kan Maman su Shuibu dakuma ni last wife dinsa ne matan da marigayi yaso yakumayi soyayya damu is a normal thing haka abun yake, gidan sarauta kenan with time zakaso Haleematu she's a good girl duk agaban mu nan ta taso and she really loves you kaman kamata asiri d'ana badai farin jini ba" Mom tai dan dariya dayasa kawai ya rungumeta tareda daura kanshi kan kafadanta wlh zaka dauka karamin yarone murya chan ciki yace "to Mom at least Baba yayi koda 7days ne kafin nafara zuwa neman wata, Mom I am still moaning my father I am not in the right state of mind to meet any girl ko talk to her" cikeda lalama Mom ta shafa kanshi tace "I know but do it for me kaji ko akwai abinda bazaka iyamin ba ni Maman ka?" Ahankali yace "babu" murmushi tayi tace "yauwa dan albarka, Oya tafi jeka shiga mota suna jiranka abaya" gyadama Mom kai yayi yasaketa ahankali wani kalan murmushi Mom take tabishi da kallo tana kara wani son yaron nata da alfahari dashi wucewa yayi yazaga baya budemai bayan wata mahaukaciyar tinted jeep akayi ya shige security yarufe kofa kallon yanayinshi Munir yayi ahankali yace "chill kawai being born from this family I guess comes with all this abubuwan" fuzar da iska Riyad yayi yakalli gefe baice komiba

aka tada motan fita daga gidan sukayi tawani secret gate basu da nisa nan da nan sukakai gidan Waziri lafiyayyen kayattacen iso aka musu aka kaisu wani lafiyayen falo suka zauna wayanshi yaciro yana dannawa kawai, Maman Haleema ce tafito cikeda farinciki tace “sannunku da zuwa Yarima Riyad da Munir sannu sannunku” anatse Munir yace “ina yini Anty” anatse shima Riyad kanshi na kasa muryanshi baya fita sosai yace “ina yini Anty” washe baki tayi kaman ta yaga zuciyanta sabida farin ciki tace “aahhh Riyad call me Mama ai yanzu anzama daya sannunku da zuwa bari naje gatanan zuwa” tashi tayi tabar falon bata wani dade da fitaba Haleema tafito tana sanye dawani ubansu exclusive atampa an mata dinki Riga da skirt daya kamata dam ajiki, ta yano karamin gyale tayi makeup tai matukar kyau da black beauty ce abinta mai kyau tana kamshi, kallo daya tama Riyad zuciyanta yakusan tarwatse, gogan yayi masifan kyau yayi wani zama kaman shugaban kasa yana danna waya abinshi batare daya nuna alamun yamasan an shigo falon ba, zama tayi kujeran dake facing nasu cikin murya mai laushe da dadi tace “barka da zuwa Yarima Riyad ina yini” ganin Riyad wayanshi yake dannawa yasa da sauri cikin barkwanci kartaga kaman yamata wulakanci Munir yace “auu ni za’a watsama kasa a ido ni hoto ne a falon nan ko Riyad kadai kika gani”? Dan murmushi tayi tace “ai kaima zan gaidaka kawai nafara gaida wanda zai kasance mijinane kuma uban y’ay’ana nan bada jimawa ba” “uh uh uhmmmm” Munir yayi gyaran murya yana kama baki sai kawai yamike cikeda wasa yace “bari naje waje abuna tunda abun hakane, nima Allah yabani tawa uwar y’ayan” yataba Riyad ganin yaki dena taba waya yace “ina waje” gyadamai kai Riyad yayi yawuce yatafi zai cigaba da danna waya dasauri cikin murya mai sanyi Haleema tace “bismillah yallabai ga abinci da abunsha na ijiye maka a dinning” dan dago idanu yayi ya zubamata su dasauri tasauke nata idanun kasa dan bazata iya jure kallonshi ba, idanunshi kaman an wanke da madara, tana wani irin jin dadi aranta kaman an gama biya mata bukatunta na duniya, daga sama zuwa kasa ya kalleta yaune rana na farko dayake kallonta baiga wani makusa ba she’s fine, educated classy but shi baiji that feeling of love da akace anaji in his heart ba, his heart is not racing, daya ganta his heart didn’t flutter, infact zuciyanshi is beating normal, breathing nashi bai chanza ba, ya kalleta and he don’t feel like looking at her again, she’s fine but batai making heart nashi fine ba, he’s not having butterflies nor goosebumps acikinshi da jikinshi, he’s not finding her intriguing dudda tai makeup etc, nothing about her is enticing his aura, he read alot barinma lokacin PHd nashi, he knows the signs of love and baiji ko daya game da itaba, he sees her just the way he sees kowace diya mace aduniya nothing special nothing different, all this look and assessment yayishi ne in secs na kallonta kawai ya dauke kai yacigaba da danna wayanshi ayangance batare dayace mata uppan ba har lokacin.

Toshi yanzu mezai fadamata? He doesn’t even know what to say, watsapp yashiga yama Mom magana yace “Mom” nan da nan Mom saiga reply tace “ya akayi yaron Mom kunkai?” Da sauri yayi typing. “yes but I don’t know what to say to yarinyar Mom” reply Mom tamai da “start conversation ask her to tell you about herself” reply yamata da “Yaya zan fada?” Mom tace “Haleema tell me about yourself” kaman zai fashe da kuka yace “too long Mom” salati Mom tabuga a chatting din tace “zan bata maka raifa tell her now!!!” Da dago kanshi yayi yakalleta karaf suka hada idanu dan kallonshi take kaman tasami video dasauri yadauke kanshi murya ciki ciki ba yabo ba fallasa yace “tell me about yourself” wani irin murmushi tayi na jin dadi tace “okay but bari nakawo maka drinks tukunna tunda bakaso kaje dinning” batare data kalleta ba

still yace “no banso” wani abu taji yanda yayi maganan bako kara amman tadaure takoma ta zauna tace “where do I even start, okay I am 24yrs, nayi sauka last 2yrs, ina karanta international relation a Oxford, ina final semester zan gama nan da 1month, ina business I have a cafe and na iya makeup but banama mutane kaina nakemawa, I love traveling too like you” tayi maganan tana kallonshi expecting reaction amman ko motsi baiyiba tace “I love having fun celebrations irin su biki, zuwa wedding dinner friends and I love shopping and I love reading novels mostly english ban iya karanta hausa books ba I think basically that’s all, ohh I have plenty friends” daga wayanshi yayi yama Mom typing tagama gayamin about herself Mom natafi ko? Dasauri Mom tace “common tell her about yourself too” ahankali yace “Mom I hate sharing u know ni nagaji i want to come back home I don’t like their house is making me feel sick” kawai yafito daga whatsapp din kafin Mom tace wani abu yamike zumbur yace “bye” kallonshi tayi kaman tahanashi tafiya tadai daure tace “tom nagode” so take yabata numbers shi koda shi bazai karbi nata ba amman bemayi maganan ba.

Yana fita yashiga mota Munir yabishi da kallo yanda yake cire boturan wuyan riganshi da sauri sauri sai kawai yahau dariya yace “banda business da yawo gari gari banga uban abinda ka iyaba Riyad wlh” wani juyowa Riyad yayi yamai mugun kallo baice komiba Munir ya kyalkyace da dariya zaiyi magana wayan Mom yashigo yakalli wayan kaman zaiyi kuka yadafe kanshi yace “ohhhh Mom nadamuna wlh” murmushi kawai Munir yayi baice komiba daga wayan yayi Mom tace “kana ina”? Ahankali yace “muna hanyan dawowa” katse wayan kawai tayi jin ana kiranta adayan wayan ganin batamata rai Riyad yakeson yi da ranan nan, ganin Waziri ne ke kiranta yasa tadauka cikin barkwanci yace “Inlaw Inlaw to Alhamdulillah, yanzun nan Maman Haleematu ke gayamin Yarima Riyad yaje yaga Haleematu da alamu akwai nasara” murmushi Mom tayi tace “eh haryama fara dawowa wai kunya, kasan fa Riyad akwai miskilanci da shegen kunya har yanzu abu yake kaman karamin yaro” dan dariya Waziri yayi yace “abinki da auta, yaro kwallin kwal, ai saisa yayi farin jini awajen kowa ina mai tabbatar miki yawanci yan kwamitin nada sarki idanunsu akanshi suke nadauka zanmasha wahalan convincing nasu amman bahaka ba wlh sunason Yarima Riyad sabida yacika sharuddan zama sarki, nafarko ga tsatso mai kyau jininshi gaba da baya asalin sarauta uwa da uba, banda haka baida any criminal record ko wani case da police ko wani abu, ga ilimi boko da islamiyya ga business daya bude dake kawoma Kano cigaba sosai dazun nan Gwamna ma yakirani kinsan Meyace mini?” Dasauri Mom tace “a’a meyace?” Dariya Waziri yayi yace “cewa yayi cikin yaran sarki waye mai manya manyan hotels din nan da gidajen mai din nan nacemai ai Riyad ne” dan dariya Mom tayi tace “ai Dodo ma nakirashi nasa yama Gwamna maganan” Waziri yace “ai ina mai tabbatar miki kaman Riyad yagama dawowa sarki dudda naga take taken Baffan su Mujitapha dakuma Kabeer amman Riyad yamusu fincikau dole ki tashi tsaye” dasauri Mom tace “tuni natashi kaga yanda ake sauka akanshi ne, duk nasamai magungunan tsari a abincin danake basa da kaikayi koma kan mashekiya” Waziri yace “yauwa hakan kinyi daidai, ranan da sarki yacika bakwai za’a sa ranar da za’a nada sabon sarki sai ayi bikin Sarautar da aurensu tare koyaya kuka gani”? Mom tace “kwarai ai duk inda zan shiga saina shiga na tabbatar Riyad yagaji sarautan nan yarona kadai ya chanchanci mulkin nan bayi yanda naga dama”.

BAYAN 1YR…..

SO WANNAN NE FIRST PART NA THIS LABARI NAKAWO SHİNE SABIDA KU GANE TUSHEN LABARIN BAN WANI SO NABATA LOKACI.

GOBE ZAMU CIGABA DA LABARIN BAYAN 1YEAR RIYAD YARIGA YAZAMA SARKI❤️

YANZU NAFARA THIS BOOK BUT YOU GUYS ARE LOVING THE BOOK ALREADY THANK YOU❤️❤️

CHAT ME UP ON WATSAPP wa.me/+2347012181461
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE8️⃣

BARI NA LISSAFO MUKU ABUBUWAN DA HABISHMA UNDERWEARS KE SAIDAWA💃
Pants(cotton, seamless, lace, spandex, plus size,thongs, gstrings etc),

Bras(nursing, padded, non padded, uk, wired, wireless, seamless, t-shirt bras, plus sizes etc)

Tights(long, short, leggings, bumshorts, laser cut tights, jeans etc)
Underskirts(silk, cotton, long, short, box, plain etc)

Sleepwears(pyjamas, adult and children pyjamas, long sleeve, short sleeve, long trousers, short trousers, dresses/gowns, character sleepwears, erotic sleepwears, enchanting sleepwears, long gowns, maternity gowns etc)

Boxers(men, boys, women, girls etc)

Vest(men, women, boys, girls etc)

Tops(chiffon tops, thick cotton tops, body hugs, etc)

Long camisoles, innercaps(plain, ribbed and chantilly), deodorant powder that guarantees 48hrs protection
CHAT THEM UP TODAY A WATSAPP KISAI NAKI💃
+2349034049623
+2348064643886

BAYAN 1YR!!

Cikeda natsuwa wasu manya manyan fadawa ke bude wani hamshakin kofa da girmanshi zaiyi girman wani karamin gate daidai karfe sha daya na safe, sannan dukansu suka fadi suka zube suna daga hannu irin yanda dai fadawa ke gaisuwa suka fara zuba kirari.
“Lafiya jakadan Baba Ali dan Baba Ali! Lafiya mai kiran gabas da yamma! Lafiya jinjirin wata sha kallo! Lafiya kwankwason jimina mai wuyar shafawa! Lafiya Garkami Wandon Karfe! Lafiya jijigen addini! Lafiya toya matsafa! Lafiya baya goya Marayu! Lafiya toron giwa! Lafiya tufaniyar gabas! Lafiya jinjirin wata shakallo! Taaaakawanka lafiya sarkin mu sarkin Riyad zakaran gwajin dafi mai hasken zuciya da hasken aura!, lafiya dan lellen Mai Babban daki…..”
Tunda suka fara kirarin nan kusan good 10min sai yanzu wani dogon mutum yafito yana sanye da wata milk kokuwar alkyabba dahar walkiya takeyi tsabagen kyanta ga rawani dawani white yadi mai kyau dake walkiya akamai, inda farare tarrr na idanunshi kake iya gani, hannunshi yarike wata sanda mai kyau, rabon da mutanen gari da yan fada suga fuskanshi shekara daya kenan, tun kafin yakaraso inda suke turarenshi yagama gauraye wajen da kamshin dadi dake dauke da yalwataccen ni’ima, ahankali yake tafiya kaman baiso yataka kasa, wani irin kwarjini shiganshi ke dauke dashi da bamaka iya kallonsa, har ya iso inda suke ya tsaya chak na kaman 5secs ya kallesu one by one to check idan kowa is healthy fine and present wanda hakan yana daga cikin abinda yasa jama’a ke sonshi, kaman baiso ya furta magana yace “kun tashi lpy”? Kaman jira suke. “Lapiyanmu kalau Sarkin mu mai adalaci, sannu sannu toron giwa tsintsiya madaurinki daya!” yanda jikinsu har rawa rawa yake sunamai kirari suna yabashi ya kalla sannan kawai yawuce duk suka biyoshi abaya, direct fada suka shige inda mutane suke cike makil wajen zama yayi ya zauna, batare daya hada ido da kowa ba this is mostly method dayayi adopting dayake samai natsuwa cus dazaran ya shigo fada he sees love hatred envy a idanun mutane da dama barinma yayanshi Kabeer, but koda wasa baitaba disrespecting yan uwanshi ba, and so far so good Kabeer din has been supportive bai bashi wani matsala ba haka ma yayyin babbanshi da Waziri ana koyamai komi everything is going smooth Alhamdulillah.

Munir sai kallonshi yake bayan yazauna, yadade baiga sarkin da mabiya keso kaman Riyad ba, anason Baban su but son da akema Riyad daban ne, har lakabi akamai da Sarki me farin jini, dudda akwai yan adawa but wlh ana sonshi barin yan cikin gari, cus kafin ma yazama sarki yana taimako sosai yasaka yara a school da dama, yanzu kawai dan he’s not happy about zama sarkin sai the whole abu yasa he hardly talks, yakara miskilanci da wulakanci fiye da da, he’s so angry sabida he’s feeling kawai responsibility akasamai akai da baya so, responsibility daya tsaya and funny enough he’s doing so good da leadership din saisa har yanzu an kasa fadin wani negative abu akanshi ko kokafadi babu wanda zai yarda ma though yasan alot of people na jiransa to just make a mistake ne and he pray dan uwanshi will not make that mistake dasukeso suke kuma jira yayi.

Almost 2hr yayi afadan sannan aka tashi yakoma side nashi, bayan an bude katon kofan nan kaman gate still akwai tafiya kafin asalin babban gininshi, baya mulki like others, he hardly let anyone a side nashi, daga Muneer sai Mom da Haleema.

Shida Muneer suka jera fadawa na binsu abaya ana kaiwa gate din kowa ya tsaya dan babu bafaden dake shiga ciki ko matarshi bata isa tashigo side dinba without izininshi, sake bude another door sukayi that will lead them to compound din da interlock ya cika ko'ina ga bishiyan mango dake wajen da flowers ko'ina sai wata arniyan jeep bulletproof dake compound din gawani secret gate dayake wajen any private outing tanan yake fita.
Shiga mainflat din sukayi WAN'ı irin crazy sitting room ne dakeda fadi na bala'in yasha funitures that are very beautiful, zama Muneer yayi yadauki laptop dake kan table yace "almost 2yrs bake leka hotel ba Riyad, its only right kaje mana" wucewa sama yayi dan yaje ya cire kayan nan dasuka isheshi.

Binshi da kallo kawai yayi kafin ya shiga replying mails, kai tsaye aka shigo falon dasauri Muneer yadago kanshi dan mamakin waye ya isa yayi hakan ganin Mom tana sanye da wani alkyabba da akayi da crystal yasa yadan taso yace "ina yini Mo…." Baima karasa gaidataba tawuce stairs tai sama fuuu.

Riyad yariga yasaka wandon wani yadi brown da farin singlet ajikinshi yana kokarin saka rigan aka bude kofan bedroom nashi, dago kanshi yayi suka hada ido da Mom data haderai kana ganinta kasan ranta abace, dan lumshe idanu yayi yakarasa saka rigan Mom takaraso ciki har zuwa gabanshi dab dashi ta tsaya cikin tsananin bacinrai tace "yau kwanan ka nawa rabonka da shiga turakan Haleema Riyad"? Hannu yamika ya dauki agogo daga saman bed yana kokarin sawa yace "Mom kinsan I've been busy dealing with lot of things, my business, this sarki thing, everything ma" "and so?" Mom tai maganan da fushi tana daga murya tace "sabida business da sauransu bazaka kula matanka ba kusan 1months da 1week baka shiga gidan ta ba, and baka bari ta shigo nan ba, sai gulma ake tell me menene banbancinka da su Muneer da basu da mata"? Dan yatsine fuska yayi still baice komiba yadauki links na hannun riganshi yana kokarin sawa Mom ta fizge links din cikeda masifa tace "Riyad wlh zan mugun sabamaka I hate this new attitude din naka, I'm talking to you baka kulani, ka shiga turakan Haleema koka kirata tazo nan your choice, people are watching and you know that, 1yr kenan kunyi aure ba ciki and it's all thanks to you, ni bantaba ganin mai gudun mace har mace ba sai kai, badadan na tambaya tacemin kalau kake functioning ba dana fara tunanin kokai mace ce" sauke kanshi yayi kasa yayi shiru why will Mom be asking Haleema irin this kinds of question? Ahankali kanshi na kasa yace "kiyakuri Mom" cikin fushi tace "nayakuri nayakuri me? Get your wife pregnant nagayamaka dagayau nakaraji kun raba kwana" ta ijiye links din akan gado tajuya zata wuce hartakai wajen kofa zata fita ahankali yace "Mom" juyowa tayi tamai wani mugun kallo saikuma ahankali ta tako zuwa gabanshi ta tsaya tana kallon kwayan idanunshi, ahankali takai yatsanta tadaura kan kirjinshi cikin kakkausan murya tace "ni mahaifiyarka na umarceka dakai tarayya da matarka, make her pregnant within period na this sabon month da aka shiga, inba hakaba wlh saika gamu da fushina sosai Riyad" tajuya fuuuu tafice yadade tsaye ahaka idanunshi sunyi

jaaa mode nashi ya chanza, he hates yanda Haleema tells Mom literally everything about marriage nasu, koma yace he hates yanda Mom ask everything akan aurensu, he hates both kawai, yana bala'in son sirri, he loves everything about shida matarshi nazama about them, anytime yakalli Haleema he doesn't even feel like shine mijinta, he feel like Mom ne mijinta, kokarin saita muryanshi yayi yadauki wayanshi dake kan gadon, Munir yakira cikin muryanshi da bata fita sosai tsabagen bacin rai yace "ka aika akiramin Haleema pls" yana maganan ya katse wayan, tashi Munir kawai yayi yafice bayan yabada sakon yashiga mota yabar gidan cus yaji komi da Mom tafadi he just pity his brother, Mom is just over controlling Riyad, she's in his matter, and baya iya cemata no, itakuma Haleema akanme zata dinga gayama Mamanshi komi gameda aurensu? Sabida taga baya iya tsallake maganan Mom ne, haba it's annoying mana, Riyad dakeda kunya tagama fallasashi, it doesn't matter koda Mamanshi ne some private mata barinma harkan auratayyan su baikamata Mom tama sani ba, the girl is sick wlh batasan menene boye sirrin mijinta ba, dashine matarshi tamai haka Allah he will deal with her, yayi tsaki aranshi.
Office yawuce abinshi inyaso yasameshi daga baya.
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE9️⃣

KINSAN YANDA AKE JIYAR DA MIJI DADI? KINSAN YANDA AKE SA ME GIDA KUKA AGADO? KINSAN SIRRIN SARRAFA TANTAKWASHIN DADI? KIN IYA HATSABIBIN KUKA? MAKIRIN KUKA? SHEDANIN KUKA DA AKEMA MIJI? KIN IYA STYLES? KIN IYA KISSA???

JOIN INTIMACY CLASS DINA WITH JUST 5K KI KOYA🔥

GROUP DIN TSAWON SHEKARA DAYA NE KIKA BIYA 5K BAKI KARA BIYAN WANI KUDI SAI BAYAN 1YEAR JUST TODAY AND BE A BADDIE FOR OGA🙈

CHAT ME UP DON SHIGA
+2347012181461
Zaune take a arnen falonta takara kiba yanzu ba kaman da datake so skinny ba, tayi bulbul taciko alamun Riyad ya iya kiwo tasami kwanciyan hankali, wasu bayi ke gyara mata farcen kafa jakadiya ta shigo zubewa tayi tace "Gimbiya Mai Martaba ya aiko akiraki chan bangaren sa" wani irin farin ciki daya lullubeta batasan sanda ta karbe kafanta ba ta mike da sauri tai sama bedroom nata ta shiga tana kiran wayan Mom awayanta kiran iPhone 15, ringing daya Mom ta daga Haleema tai wani ihu tace "Mom I love youuuu, you're the best Mom, Mom wlh ina sonki sama da tawa Mamar ma, Mom dabanda ke da narasa gata, dana shiga uku, kinga Mom

yanzun nan Mai Martaba ya aiko akirani kinmai magana ne?" Dan murmushi Mom tayi mai sauti kanta nawani swelling yanda Riyad baya tsallake dokanta, she just wish kowace uwa zatasami yaro mai taushin zuciya da jin maganan mahaifiyarshi irin Riyad kawai baya jure fushinta ko kadan ne, koyaya tace yayi abu kobayaso sai yayi, shi kawai baison commitment ne da nauyi akansa baison damuwa baison hayaniya but tace yayi kaza saiya yayine, murmushi tasakeyi tana wani ji da kanta tace "Madallah! sai a kimtsa aje, ki farantamai rai" gyadama Mom kai tayi cikin mugun farin cikin dan tana mahaukacin son Riyad tace "Mom banda kamarki me sharemin kukana, Mom thank you for making my husband to call me, bye Mom I love you" katse wayan tayi itakuma Haleeman cikeda jin dadi ta shiga shiryawa, tasha wasu magungunan da Jakadiya ke hada mata ta shiryata tsaf cikin wani hadadden atampa golden, ta daura Al kyabba akai ta feffesa turare sannan sauko kasa, Jakadiya da kuyanginta jaka biye da ita har zuwa side dinshi dayake da dan tazara tsakaninsu, tana zuwa dayake ansan da zuwanta aka barta ta shiga ciki Jakadiya da kuyangin kuma suka tsaya waje, shiga flat nashi tayi ko'ina na falon kamshin shi yake, murmushi tayi ta maida kofa tarufe sannan tacire Al Kyabban ta ijiye kan kujera tawuce sama tsayawa tayi gaban bedroom dinshi tai knocking.

Kusan yaune rana na farko da Mom take ganin serious fushin Riyad haka, and for him to provoke like this that means abinda yafadi gaskiya ne babu matan dayake nema, hankalinta yatashi sosai, wayanta dake hannunta ta daga zata kirashi saitaga wayanshi akan gado kawai cike da takaici takalli Haleema dake kuka tace "you are not sure of something akan wani dalili da rashin hankali zaki tafka shirmen nan eh Halimatu? Jibi abinda kika jawo yanzu? Bakisan idan mai hakuri yayi fushi yafi zama worst ba? Jibi yanda yafita ko wanka baiyiba bai dauki wayanshi ba tsabagen bacinrai, sabida kinga dan kunne in this pocket mesa zaki assuming mata yakebi"? Cikin kuka Halimatu tace "Mami kishi ne yarufeni I can't share mijina with anybody wlh, kiyakuri Mom kiyafemin dan Allah" dan tsukin takaici Mom tayi tace "naji is not your fault nima daban biyemiki ba nasan waye Riyad, yana tashen samartaka ma beyi neman mata ba sai yanzu, tashi kitafi side naki zansa azo agyara dakinshi lemme handle the situation" Kama hannun Mom Haleema tayi tace "Mom kinsan baya tsallake maganan ki, please kice yayi hakuri karyayi fushi dani koya chanzamin fuska" "naji tafi" Alkyabban tadauko tasaka tawuce tafita daga side din, Mom itama tafito ta tafi sauro da idanu takira babban bafaden gate din yataho da sauri ya zube yace "an gaida Mai Babban daki matan da darajanta yakai….." Mom bata bari ya karasa maganan ba cikin whispering yace "inada aiki for you Sarki baida lafiya bazai iya fitowa ba shine abinda zaka sanar kaida yaranka bansan kowa yasan Sarki bayanan, zakaga babban sakon tukuici kai haka" Gyadamata Kai yayi yace "angama me Babban daki" juyawa Mom tayi takoma ciki takira Dr su kaman da gaske, kazo gida by 10 duba Riyad".

**

1 dot tagama da hospital wanda a outpatient department group nasu yake tareda wani consultant na pediatrics, she's happy sosai yanda itada Bilal da crew dinsa na yanmata basa group daya, salla tawuce tafarayi a masallaci sannan ta linke lab coat nata tasa a bagpack tawuce tafito daga mosque din tagoya jakan abaya tasa takalmi tafito Keke napep ta tare zuwa hotel, sauka tayi tabiyashi ta shiga ciki ko kallon receptionist wajen batayiba as usual changing room tawuce tashiga cire kayan jikinta tayi ta saka dark blue dogon wandon da light blue shirt mai botur tundaga kasan rigan har sama wajajen wuya, farin fatan jikinta ya haska kayan sosai kaman dan ita akai uniform din, clean baby hijab nata farı ta dauka ta saka wanda yarufe mata kirji sannan tasa takalminta, fitowa tayi zuwa office din Madam tai knocking akace mata ta shigo, shiga tayi tace "good afternoon" "Afternoon Rashida oya ga card din jeki goge office din maza maza, ki dauko kayan gyaran office din a store" karban katin tayi tace "okay" fitowa tayi

tawuce store tahada duka abubuwan dazatai amfani dashi sannan tawuce elevator zuwa 5th floor tayi corridor office din, manna katin tayi kofan yayi kara sannan ta tura kofan ahankali hakanan kawai taji gabanta yafadi ga office din yayi mahaukacin sanyi kaman kankara AC a kunne, ahankali ta shiga tareda maida kofan tarufe cikin yar muryanta tace “wayyoo sanyi” dasauri tawuce wajen kashe AC ta kashe tanabin office din da kallo alamun an shigo dama jiya ance Oga yazo lokacin da zata tafi saisa ya shigo office dinshi kenan, a aljihunta tasa hannu ta zaro yar wayanta ta makala earpiece din a kunnenta ta danna wakan Araina Grande mai suna Into You, sannan takoma wajen kofa tadauko kayan ayyukanta tawuce bayi ta tara ruwa tafara bin wakan tafito tadauki handglove black na aiki tazura a hannu tadauki brush din share kura tafara aikinta tana waka……

Ko manager shi batasan yana nan ba babu wanda yasani sabida yanda yazo da jallabiya he looks like normal guest yawuce direct elevator, tunda yazo yake kwance dazun nan ne ma ya iya tashi yayi zuhur yakoma ya kwanta though ba bacci yakeba but ya lumshe idanu kawai having moment of peace, tunda aka bude kofan office din aka shigo yaji, sai chan kuma yaji murya mai bala’in zaki tace wayyoo sanyi, saikuma ga same muryan tafara waka tana aikace aikace dake making sound, shi kadai yace “is she some sort of DJ ko wata Artist?” Cus muryanta dadi bata missing ko harafi daya, kaman tana performing a stage, chan kuma kawai saiya tashi zaune sabida ta kunna vacuum cleaner bayajin muryan nata da kyau kaman da, karan vacuum cleaner yafi muryanta kara, ahankali yataso yataka zuwa wajen kofan hannunshi yakai ahankali zai kama handle na kofan yabude kofan sai kawai yaji yafasa cus baimason aganshi amman kuma saiya tsaya chak awajen yanajin the way she’s singing din cus takashe machine din yanzu tana bin wakan Into your arms na Witty Lowry, God! Her voice is captivating kawai yaji yakasa matsawa.

Daukan bucket na mop din tayi a hannu tarike vacuum cleaner shima a dayan hannun ta tako zuwa gaban dakin sabida tagama da office sai uwardakan before wanke bayuka, juyar da fusknata tayi tana ijiye vacuum cleaner akasa still holding on to the bucket na mop takai free hand din tabude kofan ahankali fuskanta na kallon side din tana rera waka tadawo da hannun tana kokarin daukan vacuum cleaner back danta shigo tunda tabude kofan…

Tunda tabude kofan yayi setting eyes nashi chak akanta yana kallonta tundaga kan pink crocs din dake kafanta dayay finding nasu so funny, dogon dark blue wandonta dabai kamata ba at all kusan ma yaso yamata yawa ya kalla, zuwa navy blue rigan dashi ma bai kamata ba zuwa farin hijab din jikinta that looks extremely neat da side na face nata da he could see sajenta da dan

gashinta baki sidik daya leko, daidai tadaga vacuum cleaner ta juyo da kanta kawai taga dogon farin mutum da farin jallabiya ajikinshi ya tsaya chak kaman gunki yazuba hannu a aljihun jallabiyan yana kallonta batada tsoro but saida ta tsorata tayi baya da sauri ganin namiji hakan yasa cord (wayan) vacuum cleaner ya kwasheta jikake timmm tafadi akasa ruwa mopping din hannunta ya kware mata daga ciki zuwa wando, zaro ido tayi atsorace tace “wayyoo Allah na” tai maza maza ta tashi tama rasa mezatayi arude tace “I am sorry” ganin kaman ba ghost bane maybe shine me hotel din takai hannu tana kakkabe jikinta da cinyanta da sauri chan ta lura da aljihuta ajike dasauri tace “Innalillahi wayana” hannu tasa a aljihun taciro wayanta ta cisge earpiece din tashiga tattaba wayan baya haske tace “innalillahi Innalillahi” bude wayan tayi da sauri taciro battery ta huhure wayan sannan tawuce table dagudu ta ijiye wayan awajen danya bushe sannan tajuyo tama kasa kallonshi taduka tana daukan mop tace “sorry i will clean everything yanzu” chak yake kallonta dan yana ganin full fuskanta ya ganeta the girl from the airport! The feisty gurl! Yarinyar daya dade yana nema to reward her for saving his life….

GOGAN NAMU BATA GANESHI BA? KODAI IDONANE💃🤨
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 1️⃣2️⃣
Bucket na moping din tadauka da gudu tawuce bathroom na office din  ta tara wani ruwa ta taho da sauri jikinta duk rawa yake zata fara mopping ruwan kunfan kasan jikinta duk yana tsiyaya kaman daga sama taji sassanyar muryanshi yace “stop!” Dasauri tadago manyan fararen idanunta ta kalleshi, hada ido tasakeyi dashi for the second time da sauri ta dauke kai aranta tace “sai shegen kallon mata mtsww” fitowa daga dakin yayi ahankali, cikeda tsantsan kulawa yace “step aside” dasauri ta matsa gefe ga mamakinta sai kawai taga ya tsugunna yadauki bucket na mop din ya matsar gefe da vacuum cleaner, yashiga nannade carpet din na tsakiyan office din yadaga yadauka yawuce wajen kofa yabude yafitar dashi ya ijiye bakin kofan nan yashigo yasameta tana kokari fara mopping wajen cikin kwantacciyan murya yace “go and change” dan kallon daga kasan riganta har zuwa crocs na kafanta tayi  dake tsiyaya tace “karka damu I can do it banda wani uniform, zai bushe ai” yanda take kallon jikinta tana maganan yake kallo with her voice dake piercing kunnuwa sabida dadinsu, calmly yace “go take them off kisa kayan gida” kawai dan tasan office din mai hotel dinnan ne, sannan shita gani cikin offive din so dole tai assuming shine mai hotel din banda haka data gayamai me ruwanshi da yanda zatai aikinta yabarta tayi abinta tagama mana ha’a, sai gwadamata yanda zatayi yake, sai kawai tawuce kofa batare datace komiba tana zare handglove din, tabude kofa tafita yabita da kallo kafin kawai yazaga yazauna kan kujeranshi na office yayi shiru.

Changing room dinsu tawuce ta chanza kayan tasaka doguwan rigan atampanta brown ne da

milk just straight gown babu wani ado ajiki, dan kwalin kayan ta daura aka sannan ta zari gyalenta brown ta yafa daya kara haskata hasken fatanta yayi bau aciki, ta kwashi kayan bayinsu na staff ta shiga ta dauraye kayan ta wanke cinyanta da kafanta da takalmin tama wanke fuskanta kawai gaba daya hakan yasa tai wani haske mai kyau dinnan na bayan ka wanke fuska, tawuce baya ta shanya kayan sannan tafito tana tafiya da sauri sauri sabida tasamu tai sauran ayyukanta tabar office dinshi, tashiga elevator zuwa 5th floor tawuce office din kofan office din ta bude ahankali tashigo tunda ta bude office din ya kafamata ido, the first time daya ganta uniform ne jikinta, yauma haka yanzu ne yafara ganinta da kayan gida, kasa dauke idanunshi yayi akanta, ta taho direct cikin office din batare data kalli wajen dayake bama, zubamata idanu yayi yana kara tantancewa itace dai wannan mara kunyan ta airport, bai cika manta face ba idan yasan mutum, hade fuska tayi batacemai komiba dan jikinta yabata kallonta ake, tadauki moping stick din tafara moping wajen ahankali tana gamawa tadan juyo ta kalleshi karaf suka dake hada ido dauke kai tayi tace “zan iya shiga dakin na gyara”? “Yes” ya amsa calmly hakan yasa kwai ta shiga ta sharo tai arranging bed din dataga ba’a gyare ba, ta wanke bathroom din, kusan 5min tayi sannan tafito tawuce bayin nan office ta gyara shi in 3min sannan tafito tai arranging abubuwan datai amfani dasu tafita dasu waje sannan tadawo tazo gaban table dinshi tasa hannunta tana kwasan wayanta na wajen yanabin white long fingers dinta da kallo that looks so feminine, ahankali yace “wat is your name?” Batare data kalleshi ba tace “Rashida Almustapha” tana maganan tajuya dasauri zata wuce kaman daga sama yace “is your back hurting you naga kin fadi tabaya”? “No it’s not” tabashi amsa atakaice tacigaba da tafiya da sauri bataso yayi wani maganan kuma, hartakai kofa tasa hannu zata bude yace “Rasheedahhh!” Wlh batasan meya faru ba hakanan gabanta yafadi chak ta tsaya takasa motsi sabida yanda yakira sunanta, kawai she felt something strange in her dayasa dasauri tajuyo ta kalleshi sake hada ido tayi dashi saikuma ta dauke kai tace “na’am” kusan 30secs yayi shiru saichan ahankali yace “Thank You” Da sauri ta kalleshi zatace thank you for wat saikuma ta tuna maybe na gyaran ne hakan yasa ta gyadamai kai kawai tama kasa magana sabida yanda heart nata yafara racing tajuya tafito dasauri ta kwashi komi tawuce kasa ta maida komi store tawuce taje dakunan dazata chanza duvet nasu takai washing machine takai sannan tahau gyara Allah yasota bata hadu da Madam ba balle ta tambayeta ya akayi tasa kayan gida ba.

Wuraren 6 tafito daga hotel din sai fama take da wayanta dayaki kunnuwa sai cire battery tana maidawa take sabida ya kunnu yaki kunnuwa, ga jakanta goye abayanta. “Hi Rashy” Aisha receptionist dake night zuwanta kenan tai waving nata tana murmushi awkwardly tadaga hannunta saikuma ta maida ta gyada mata kai kawai tawuce tafito waje tana hure huren waya, Munir da Riyad na tsaye awaje wannan karan ya chanza kaya zuwa jumper na milk yadi suna magan kaman daga sama ya hangota tafito tana hura wayanta, yanda hankalinshi da attention nashi yatafi wajenta saida Munir yajuya dasauri dan yaga meyake kallo haka ganin wacce yake kallo wacce kallo daya yamata she looks like worker nasu not guest yasa yace “who is she?” Batare daya dauke kanshi daga kallonta ba yace “my savior” dasauri Munir yadauke kanshi daga kallonta ya kalleshi dasauri yace “kaman ya your savior?” Yana kallonta yace “the girl that saved me from those goons a airport” dasauri Munir yajuya ya kalleta yace “wow the clearner

damuka dade muna nema wat a small world ashe anan hotel namu take aiki, but did you tell her”? Girgixamai kai yayi daidai tasha kwanan layin yadauke kanshi yace “No bangayamata” Munir yace “why?” mota yashiga yace “bata ganeni ba” tada motan Munir yayi yace “ai da saika gayamata, How will you reward her yanzu?” Kai tsaye yace “I will ask her kome takeso arayuwa i will grant her any wish take da shi she’s part of the reason I’m alive today” murmushi Munir yayi yace “wat got you so angry today?” Yatsine fuska yayi yace “I don’t wanna talk about it” ahankali Munir yace “to mutafi gida? Mom tasa an sanar bakada lafiya just to manage situation din harda kiran Dr, tace na tabbatar mun dawo gida tare” hannunshi yasa yasauke glass na window ya lumshe idanu bai sake cewa komi ba, ganin baison magana yasa yace “azumi saura 7days fa bakai approving fund na kayan abincin daza’a rabama al umma da ma’aikatan ka ba” dan ijiyan zuciya yayi yace “i forgot bani file din da pen lemme sign” ahankali Munir yace “bari mukai i will give u yana file dake back seat.
JOIN GROUP DANAKE POSTING

https://chat.whatsapp.com/Ckm5Bo7CcqR1NYkgT0HEvR
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣3️⃣

Gida tashiga around magrib agurguje tai alwala tashigo ciki Mama nakan dadduma hakan yasa ta tsaya kusada ita ta kabbatar sallan.

Tana idarwa cikeda damuwa tace “Mama ruwa yashiga wayana taki aiki wlh” tai maganan tana jawo jakanta taciro wayan cikeda damuwa itama Mama tace “garin yaya meya sameta?” Cikin damuwa tana kara huhhure wayan tace “faduwa nayi ruwa ya kwaromin shine ruwan yataba har wayan” dasauri Mama tasa hannu ta karbi wayan itama tana huhhura duk wani huji na wayan ta maida battery din kozata kunnu amman bata kunnu ba hakan yasa ta tashi tawuce chan wajen yan kayan abincinsu tabude ledan shinkafa tasa wayan ta zuba shinkafa akai tace “bari mugani kozata kunnu idan bata kunnu ba saina tattara kudin dake wajena kije ki sayo wata wayan dashi, kina bukatan waya kodan school, Allah kiyaye bakiji ciwo bako”? Gyadama Mama kai tayi tace “banji ciwo ba” Mama tace “to ai mun gode Allah tashi kiyo wanka kici abinci” dasauri tace “Mama girki kikayi”? Gyadamata kai tayi tace “eh nayi shinkafa da wake da mai sa yaji” murmushi tayi tace “Mama banace ki dena girki ba” ture mata hanci Mama tayi tace “to banji maganan ki ba Anty Rashida” kwashewa da dariya tayi hakan bakaramin dadi yama Mama ba ganinta duk cikin damuwa sabida wayan tasan lissafi take ta yanda zata taba kudin saving dinsu tasai waya dashi kafin takara samin wani kudin fa, rashin lafiyan Mama fa, abinci fa, kudin wuta fa, tasan duk abinda take tunani kenan ganin tayi dariya yasa hankali ta ya kwanta, cikin shagwaba tace “kai Mama nine Anty Rashida” Mama ta kama haba tace “yooo ai hakane,

Mama karki kaza, karki kaza, kullum command kike bani yarnan kinga ai kinzama Anty Rashidan” sake bushewa da dariya tayi kawai saita kwanto jikin Mama tace “Mama stoppp wlh ni ba Anty Rashida bane, Mama ina hanaki ne fa sabida karki fadi, kinga kinada yawan ganin jiri, kınada migraine kuma, Mama I have to take care of you gwara namiki komi ko ruwan dazakisha na ijiye kusa dake sabida karki wahala wajen daukowa” tabe baki Mama tayi tadagata daga jikinta tace “jeki wanka kizo kici abinci” tashi tayi ba musu ta rage kayan jikinta tadaura zani ta kwashe kayan da lab coat da kayan Mama data cire yau dasafe tafito saida ta fara wankesu tsaf ta shanya sannan tawuce bayi tai wanka tadawo Mama tabata abincin ci tayi bawani sosai ba batawani cin abinci abin yabi jikinta sannan takai kwanon waje ta kuskure baki ta dawo tahau salla kusa da Mama tana idarwa ta kwanta awajen ko 2min ba’ayiba tafara minshari Mama tai shiru tana kallonta sai kawai tasa hannu tadauki feet dinta ta daura kan cinyanta dudda uban tafiya akasa datakeyi bata da kaushi kafanta still looks very fine ga nails dinta farare kal masu kyau, ahankali take massaging kafafun ayanda ta gyara kwanciya kasan tanajin dadin tausan Mama is just looking at her babu salloli biyar dazatayi arana da zatakai goshinta kasa dabazatama Rashida addu’a ba, banda kiyamun Layli datakeyi kullum, kullum addu’an ta shine Allah yakawo ma diyarta karshen wahalan nan Rashida ita ke ciyar da ita, itace cinta shanta suturanta magungunanta da komi na rayuwan su Rashida ke nema,  babu yanda zatayi ne dan batama da karfin aikin ne da itace zata fita ta nemawa diyarta abinci da komi ba diyarta tayi ba, kullum addu’an ta is Allah ya tsare yarinyar ya tsare imaninta kar wata rana tagaji da aikin wahalan nan tace zata shiga duniya tabi maza dan shine hanya mafi sauki da akebi asami kudi, addu’anta koda yaushe shine Allah yabata ikon kammala wannan karatun likitan, kowani shekara da hayya hayya take tara kudin school fees nata na last year bai musu wani wahala ba sabida tasami aikin hotel din nan ana biyan ta dubu 50k duk wata a nan ta tattara tabiya, fatanta shine Allah sa wannan shekaran na biyar kar kudin makarantan yayi yawa dubada yanda aka kakkara kudin makarantu, hawaye ta share ahankali daya zubo mata bata taba sanin dan Uwanta na jini zai iya juya mata bayaba sabida wannan cutan dudda da ranshi da lafiyanshi, bata da kowa sai Rashida, yau shekaru ashirin da uku kenan tana wannan wahalan tun Rashida na cikinta, ta haifo yarinya cikin wahala ta tashi cikin wahala sannan itama tana rayuwan wahala, batabama yarta komiba sai wahala, babu wanda ya yarda ya auri Rashida, ga yanda yar karaman yarinya ke aiki kaman namiji wata kalan uwace ita, hawaye ne suka kara zubo mata sai kawai ta jinginar da kanyon a bango takalli sama murya chan kasa that is very weak tace “Ya Allah idan mutuwata shine mafi alkhairi agareni dakuma y’ata, idan mutuwata zai cireta daga cikin wahalan nan datake ciki Allah ka kasheni, ka aurar da Rashida gidan dazata huta,  karufama Rashida asiri, ka lullubeta cikin nimarka Ya Allah.

Tadade ahaka yawanci tana boyema Rashida damuwanta da dama sabida kar yarinyar takasa karatu idan kanaso kaga Rashida ta birkice tarasa sukuni to Mama tace kaza namata ciwo tuni yarinyar zata rude, damuwa, tunani ga constant ciwon kai koda yaushe shiyafi damunta, saisa kullum tane asibiti BP ta is high, magungunan BP nema ke cinye musu kudi cus maganin HIV free ake bata a clinic dinsu.

Ganin yanda bacci ya shigeta yasa bata tadataba tabarta tai baccin anan kan dadduma.

Wuraren 5 Mama ta tadata da kyar ta tashi wanda hakan daman is daily battle nasu, gyaran gidan tayı tasa takai Mama tai wanka tai salla tazo ta dumama shinkafa da waken sannan tama Mama tuwo sunada miya daman kafin ta shirya cikin bakin abaya da stones nashi yagama fita tass but dudda haka ya mugun mata kyau abunka da fara tazo taje wajen wayanta taciro daga shinkafan tasa battery ta kunna amman still yaki kawowa Mama tace “bai kawo ba?” Gyadama Mama Kai tayi ahankali, dasauri Mama tazo karban wayan tayi tace “kodai ba chaji ne” tawuce wajen chazanta dake bango ta makala kusan 3min bai dauka ba, ahankali Mama ta tashi tace “bari nabaki dubu talatin din nan saiki sayo wata wayan kawai” dasauri tace “a’a Mama ki adana talatin din nan, bari zan kaita wajen yan waya a gyaramin zasu iya gyaramin” badan Mama taso ba dan wayan tariga tagama tsufa dukta farfashe tace “to shikenan bari na baki kudin gyaran” sip tabude taciro wani leda ta kirgo 5k tabata karba tayi sannan tayafa gyalenta tace “bye Mama” har zaure Mama tarakota tace “adawo lpy” dayake 9 ake fara clinic dinsu hakan yasa taje shagon Maman kuwa tayi aiki ta karbi 2k dinta sannan tawuce shan wajen gyara takai wayan ganin zai dauki lokaci tace “zata dawo da yamma” tashiga keke sai hospital nasu.

she’s not really doing much a consulting room take zama attached to consultant din da aka assigning nata to him yana duba yara marasa lafiya yana tambayanta me aganinta take tunanin is diagnosis din tafadi, kokuma yace wani investigation yakamata ayima yaron tafado sunayen series of test da za’ayi ganin how brilliant d girl is tsohon likitan yace “i will comfortably leave the office for you tommorow” gyadamai kai tayi dan she hardly smile outside, haka dai tagama by 1 tawuce mosque tai salla ta linke labcoat tasa a bag sannan tafito tashiga keke sai hotel.

Yau tadanyi latti sabida traffic sai around 2:30 tashigo hotel din ko kallon mutanen dake reception da lobby gabaki daya batayi ba da sauri sauri tawuce changing room nasu kofa tabude ahankali, ma’aikatan su tagani gudu uku a lobby suna chanza kaya da kallo suka bita batace musu kala ba tawuce locker dinta tasa password dinta tabude, daya daga cikinsu ne taja tsaki tace “mutum sai fadin dai, nagadai da mutum dan wani ne dabaizo hotel neman aikin shara da wanke bayi ba, tundadai duk ansan juna menene na jijji dakai kaman diyar wasu” ? Sauran biyun ne suka kwashe da dariya daya tace “dadine dake Hussy baki hadiye abu aciki” parking gashinta tashiga yi da ribbon tace “eh mana kullum fuskan mutum amurtuke ana fadin rai ana daga shoulder kaman yar shugaban kasa amman shine akazo aikin wanke bayi a hotel” wani irin buga marfin locker Rashida tayi saida yayi kara pammm!Tajuyo tai facing Hussy direct cikin zafin rai tace “dani kike maganganun nan?” Wani banzan shakiyin kallo Hussy tamata dan tadade tanajin haushin Rashida wai ace ma’aikata nawa a hotel din nan yarinya bata kula kowa, kuma kai kasauke kanka ka kulata taki kulaka back, bama wannan yafi bata mata rai ba yanda take nuna bamatasan anyi hallita irinsu a wajen ba ko ka kulata ita bazata kulakaba sai bakin

taurin kai, jibidai yanzu datazo tasamesu ko Hi bazata iya gayamusu ba? Amman basu isheta kallo ba, cikeda tsana tace “naga dai ban kira suna ba, amman duk wanda ya tsargu dashi nake” wani irin kallo Rashida tamata kaman taci ubanta saikuma ta tuna nan wajen aikin tane, da kudin aikin wajen nan zata biya school fees and other things bari kawai ta barta today is her lucky day, sai kawai tajuya tasa hannu zata dauki uniform nata batare data kara magana ba, cikeda neman fada Hussy tai wani shewa tace “jakan ta tsorata” juyowa Rashida tayi da mugun zafin rai batai wata wata ba ta fizgo gaban rigan Hussy ta kifa mata mari a fuska ihu jikake tasss! Hussy tayi ihu ta chakume gaban rigan Rashida tace ni kika mara”? Sai dambe, dukanta Rashida take bana wasaba har gyalenta na fadi kasa bakin gashinta datai parking donut mai bala’in kyau ya bayyana, sauran yammatan biyu na kallo sunajin dadi ganin suna dakan juna dudda Rashida nacin uban Hussy amman kallon fada da dadi yake sukaki rabasu, ganin jini Rashida tafasa bakin Hussy yasa daya cikinsu ta tsorata tace “baruwana kar ayi kisan kai agabana” dasauri tabude kofa tafita da gudu dayan ma tabiyota hango Madam sukayi a lobby tana magana da receptionist kafin sukai wajen ma sukai ihu. “Madam ana fada” daidai lokacin Munir da Riyad na shigowa yana shaye da brown jumper yasa brown shade a idanunshi na CK dayamai kyau sosai, arude dayan tace “Ma come oo harda blood everywhere!” ganin Riyad yasa Madam tace “Sir welcome wai ana fada I don’t even know with who lemme handle it” tawuce jin yasa Munir yace “let’s intervene” Munir yayi gaba Riyad yabiyosu abaya yana tafiya one one a kasaitance, da gudu Madam ta shiga dakin tai ihu “what is this”? Ganin blood har wuyan Hussy, Rashida bama tasan an shigo bama Munir yashigo dakin daidai Riyad na isowa chak ya tsaya wajen kofan batare daya shigo ciki ba yana kallon su, jan Rashida Madam ta shigayi da karfi gaske ganin yanda take dukan Hussy, sauran yan aikin suna banbare hannunta daga jikin Hussy sunajan Hussy da bakinta yayi jina jina da jini harda hanci baya suka kwasheta da kyar daga hannun Rashida, Madam data rike Rashida cikin tsananin bacin rai tace “fighting awajen aiki are you too Mad? Rashida wat is this why did you beat her up like this?” Itafa idan tana fushi bata gane kowa, kabar da hannun Madam tayi daga jikinta a haukace kaman ba Rashida ba cus ranta yabaci tace “dalla sakeni kekuma Malama” tajuya zata closet nata cikeda taurin kai duka ma’aikatan har Munir saida yakalli Rashida yasake kara kallonta jin abinda ta gayama Madam, Hussy dake haki an riketa tace “Ma kinga halinta ko saisa all worker ke cemata psycho, kolomental ce wlh, mahaukaciya ce very weird girl, shegiya yar shaye shaye, an gayamiki bamusan asalinki bane, uwarta nada HIV!” Chak Rashida dake tafiya ta tsaya kaman kankara, ihu Hussy tayi ganin ta tsaya chak da tafiyan datakeyi that means maganan ya shigeta tace “ai duk munsan sirrin ta Ma, harnan akazo tundaga layinsu aka gayamana we should be careful with her tanada HIV Mamanta ma nadashi, bamu gayamiki ba Madam sabida karki koreta cus munsan she needs this job for her virus drugs da Mamanta, amman shine zata kama dukana ba ban mata komiba bayan tanada wacce tafi chanchanta adaka islamically agida, diyar fasika kawai!” Wani irin juyowa da Rashida tayi zaka dauka zakanya ce ta taho da gudu tareta Madam tayi tace “where do you think you’re going” wani irin hankada Madam Rashida tayi saida Munir yatare Madan da sauri dan inda tafadi wlh saita karye, Hussy na ganin haka ta wuce da gudu tabi gefen Riyad ta gudu tafice da gudu Rashida ta taho itama tsabagen fushi ko ganin gabanta batayi ahankali Riyad yadaga kafanshi yashigo ya tare kofan yayi blocking nata, hakan yasa ta dago jajayen idanunta takalleshi adake cikin tsananin fushi da zuciya tace “ka tashin mini daga hanya” Madam da Munir ya daga kyar tace “it seems da gaske

yarinyar nan is mad, call security namu and call the police” yana kallonta ta glass batare daya dauke idanunshi daga kallonta ba yace “don’t call anybody” cikin kumfan zuciya kaman zata fashe tai wani irin ihu tace “nace ka tashinmini daga hanya” strictly yace “you’re not going anywhere!” Wlh ayanda zuciya ke daukanta kaman ta dagashi ta yar takeji kawai tasan batada karfin ne, yanda hannayenta ke rawa da jikinta yasa kawai ta juya fuuuu tawuce dan bence din dake wajen ta zauna tai folding hands dinta akirji duk yan dakin kallonta suke she’s shaking, sai alokacin yakalli Munir yace “get first aid box go and attend to that girl, yakalli Madam da sauran yar aikin dake kallon Rashida da mamaki kaman yau suka fara ganinta yace “ku wuce kutafi” cikeda mamaki Madam tana kallonta tace “this is your last day here” duk wucewa sukayi suka fita yarage Riyad kadai dake tsaye awajen kofan dan kwalinta dake kasan dakin ya kalla ahankali ya shigo ya duka gently yadauka dusting nashi yayi sannan yataho inda take zaune kanta akasa tayi folding hands a kirji ahankali ya yafa gyalen akanta.

Dago kanta tayi tazubamai jajayen rinannun idanunta yanda yara masu taurin kan nan sukeyi tace “ina ruwanka dani? Wayace katabamin gyale na? Wat is your business with me? Nabar aikin naku dagayau nima, bazan kara aiki inda wata ta kira Mamana…….” Saita kasa karasa maganan sabida yanda abin ya tsayamata awuya saikawai tajuya mai baya da sauri takai hannunta ta sharce hawayen daya soma zubomata, data sharce da wani yasake zubowa sunki tsayawa yakai almost 1min yana kallonta sannan yajuya ahankali yafice tareda maida kofan yarufe kaman jira take fashewa tayi da kuka haryafara tafiya yajuyo sautin kukanta chak ya tsaya har shesheka takeyi yakai kusan 1min ahaka sannan yabar wajen, kusan 5min tayi tana kuka sannan ta goge fuskanta tass ta tashi tawuce drawer ta ta shiga kwashe yan small small tarakacen datake dashi awajen uniform nasu tabar musu sannan ta goya jakan abaya ta tsaya takara goge fuskanta tass bazaka gane tai kuka ba unless u look into her eyes tafito sai kallonta ake a reception amman ko kallonsu batayiba ta wuce tafita ta tafiyanta gida.

JOIN MY WATSAPP GROUP
https://chat.whatsapp.com/Ckm5Bo7CcqR1NYkgT0HEvR
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE1️⃣4️⃣

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/ChfonTBUkdg8q2KIWCSk46 Assalamu alaikum. my name is Faredah Haruna Mamuda the founder of REEDAH'S EMPIRE, i base in kaduna state we are your number one home appliances no (SCAM ZONE) we are 100% legit all our items are from

Lagos,Egypt,Turkey and cortonor we do delivery nationwide thanks u'll

Wuraren 3 Mama na zaune tsakar gida tana gyaran shinkafa ta kunna radio ta ijiye gefenta saman tabarma tana sauraro taji an turo kofa an shigo hakan yasa ta kafa ido taga wazai shigo bakuwa tayine saitaga Rashida sosai gabanta yafadi ganinta cus bata taba ganin Rashida ta shigo gida around this time ba, kallo daya ta mata tagane tai kuka dawuya ne Rashida tama wani abu tai kuka, ita kadai ke iyasa yarta kuka dasauri ta ijiye tray shinkafan tace “lafiya menene kika dawo dawuri haka?” Murmushi ta kakalo tace “Mama kaina ke ciwo sosai saisa nadawo” tai maganan tana zama kusada Mama kanta Mama ta taba tace “bari na kawo miki vitamin C kisha tashi ki cire jallabiyan kisha iska” tashi tayi tawuce ciki Mama tabi jakanta dayay strange girma da kallo sai kawai ta jawo tabude ganin karikitan ta ne ciki yasa da sauri ta tashi tabita daki tana tsugunne gaban ganamasgo tana neman kaya Mama tace “an koreki wajen aiki ne”? Dago kanta tayi ta kalli Mama zatai magana Mama tace “karki kuskura kimin karya an koreki daga wajen aiki ne?” Ahankali tace “Madam dina tace yau ne last day na aiki na a hotel dinsu” waje Mama tasamu dasauri ta zauna jin jiri zai dibeta tace “Meya faru tell me everything” Mama tariga ta ganota hakan yasa tafadima Mama komi ba karya, ba karamin baci ran Mama yayi ba tace “sau nawa zan gayamiki ki dinga hakuri arayuwa Rashida eh? Zagi na kari ne? Koko zagi na nunawa ajiki ne? Dan an zageni sai mene” dasauri Rashida ta kalli Mama, Mama tace “yes dan wata ta zageni and so wat dazaki hau fada awajen aikin ki kina hankade Madam dinki har sau biyu mai hotel din gabaki dayama shima kinmai rashin kunya” ahankali takai hannu ta goge hawaye tace “Mama bazan iya daurewa azageki agabana ba ko ace wani abu mara kyau wlh” saikuma tarushe da kuka tace “narasa me nayima yan layin nan duk inda nake aiki sai sunsan yanda sukayi sukaje suka batani su fallasani, wlh kowaye meyi ban yafemai ba” tabama Mama tausayi amman kawai saita wuce tabude drawer tadauko hijabinta har kasa ta saka da sauri Rashida ta mike tace “Mama ina zaki?” Cikin dan masifa tace “ina zani? Ina kuwa zani inba wajen aikin naki ba naje nabada hakuri itama yarinyar a nunamin gidansu naje nabada hakuri, idan babu aikin nan tayaya zaki gama makarantan ki eh? Me zamuci? Dame zaki sami kudin siyan tufafi? Ga wayanki ta lalace baki dawo da itabama that means bata gyaruba duk ina zamu samu kudin nan kafin kisami aikin nan kin manta kalan wahalan dakikayi eh? To zuwa zanyi nabada hakuri” dasauri ta taho takama bakin hijabinta tace “Mama dan Allah dan Allah karkije kinji Mama” fizge hijabinta Mama tayi tace “inda bakiso kisani naje nabada hakuri ai da bakiyi abinda zai tursasani inje ba, yau ko basu karbeki ba dolena naje na bada hakurin abinda kikayi kinma mutanen dake gaba dake reni sannan kin fasama yar mutane hanci da baki” baki Rashida tabude zatai magana Mama ta nunata da hannu tace “kimin shiru anan” ta fiziğe hijabinta tajuya tafita fuu Rashida nada zuciya so tasan yarinyar didn’t even realize how important this work is to them most especially towards karatun ta she will do everything ta tabbatar Rashida tagama karatun ta lafiya.

Kafa Mama tasa ahanya tana tafiya ahankali kanta na sarawa amman ta daure cus she knows what school din Rasheeda means to her, she will not allow her to sabotage mean na school fees payment nata ba, she just hopes darajanta zaisa sumata afuwa.
Tanakai junction ta tare keke da taso taje da kafa ne, amman taji jiri na dibanta bazata iyaba,

har hotel din aka kaita ta sauko tabiya kudin tajuya ta kalli tamkeken hotel din almost duka inda Rashida take aiki ta sani musamman take binta dan tasan inda diyarta ke aiki incase wani abu yafaru she knows inda zataje neman diyarta amman bata taba shiga wajajen aikinta ba, ijiyan zuciya ta sauke jin yanda heart nata ke beating saita dan natsu kafin ta shiga building din motoci cike anyi parking, hotel din yahadu bana wasaba, karasawa tayi zuwa entrance door din zata shiga from yanda take looking security guard dake gadon kofan shiga reception din yace "Hajiya wakike nema? Idan zancen taimakone Oga yace jibi ranan juma'a za'ayi rabon abincin azumi you can come by 10AM" ahankali Mama tanuna kanta tace "nine Maman Rashida sannunku da aiki, Rashida na aiki anan maybe kasanta, to tayi laifi ne shine nace bari nazo nabawa Oganta hakuri dan Allah akomar da ita sannan nabama yarinyar hakuri" kallon Mama sukayi sannan suka kalli juna kafin daya ya nuna mata kujera dake chan gefe wani plastic chair yace "guest da ma'aikata kadai ke shiga ciki jeki zauna achan Oga nada baki amman zai fito anjima kadan sai a gayamai" Mama batai musu ba tace "toh" wucewa tayi zuwa kujeran dasuka nuna mata ta zauna tabuga tagumi tai shiru burinta kawai karsu kori Rashida addu'anta kenan, gabanta sai faduwa yake cikeda fargaba.

Tunda yaje office nashi yayi shiru bakin dasukayi ma yawanci Munir ke kulasu, agogon hannunshi kiran Rolex ya kalla 5 tayi na yamma kaman an tsikaresh ya mike duk kallonshi sukayi "excuse me" yafadi tareda wucewa wajen kofa yafice Munir yabishi da kallo kafin yacigaba da abinda yake samin kanshi yayida shiga elevator ya sauka kasa, he doesn't even know why he's doing this but samun kanshi yayi da zuwa hanyar changing room din ganin kofan wangale abude yasa yadan leka ciki babu kowa wajen fuzar da iska yayi yajuyo yafito daidai Madam zata shigo hanyar chak ta tsaya ganinshi surprisingly tace "Yallabai wani abu kake bukata"? Kaman bazaiyi magana ba saikuma yace "where is she"? Kallon hanyan Madam tayi tace "wa she? Oh mahaukaciyan nan"? Dan lumshe idanu kadan yayi hakanan yaji kalman azuciyanshi yadai daure bai nuna wani abuba ya kalleta, dasauri tace "ta tatare kayanta ta kwashe komi na locker ta tatafi tabar aikin da kanta kafin mu mata official kora"  yanda taga yahade fuska yasa dasauri tace "sorr…." Ahankali yace "sack the other gurl Hus…." Cikeda Mamaki Madam tace "Hussyn Yallabai"? Babu wasa akan fuskarshi yace "I don't want her working for my company, just compensate for the injury, give the other gurl a call tadawo aiki" yana maganan yawuce baki Madam yakasa kulluwa tana kallonshi, yarinyar data barar da ita yake cewa akirata back, wacce aka jibga yayi sacking, dan ijiyan zuciya tasauke aranta tace "his company his rule!" Tawuce ta tafi office nata.
Wucewa kawai yayi yabar wajen yafito, security daya budema wani guest kofa dazai shigo ne ya hango yallabai hakan yasa yashigo ciki da gudu daidai zai shiga elevator yace "Yallabai barka da hutawa dama wata mata ke nemanka awaje" wani kallo Riyad yamai irin wata wa? Shi kuwa? Dasauri security yace "tace wai itace Maman yarinyar da aka kora tazo tabada hakuri tana waje, she's Rashida's Mom Sir" hakanan Riyad kawai yaji gabanshi yafadi but yadaure yace "why is she sitting outside?" Dan sauke kanshi kasa Security yayi yace "uhmm Yallabai

cewa akayi cutan kanj……" fuuu Riyad yawuce zuwa entrance door din kafinma abudemai kofan dayake glass door ne yana iya hangota yanda tazauna kan kujera tayi tagumi tana kallon waje daya cikeda tsananin damuwa and kana kallon matan kasan she's really sick she looks so skinny and pale jiyayi zuciyanshi yamai ba dadi sosai yanda security sukai trashing nata awaje haka, dasauri yafice bayan an budemai kofan yayi wajenta direct yana zuwa kawai saiya duka cus bemasan mezaiyi ba, she's the mother of the girl that save his life kome yayi bai biyataba, cikeda girmamawa yace "Mama" firgigit Mama tadawo daga dogon tunani datake tajuyo ta kalleshi, dasauri tace "Naam Bawan Allah kaina mai wajen nan nazo nabada hak….." kafin takarasa maganan dasauri yace "Mama" hakanan Mama taji yanda yakirata yataba zuciyanta, yanda yakira sunnan just touched so many things a zuciyanta kawai sai hawaye, life and sickness nata have made her so emotional, muryanta na rawa tace "dan Allah dan Allah kuya kuri nasan Rashida da zafin zuciya ga fada ga taurin kai, kome akace tama yarnyar nan nasan tayi dan Allah kuyakuri kurufamin asiri kada ku koreta daga aikin nan dan Allah ku taimakeni" tai maganan tana jan kujeran baya zata duka dasauri Riyad yakama knees nata ahankali yace "Mama dan Allah karki rokeni, ban koreta ba zata iya cigaba da zuwa aiki" da sauri Mama ta kalli fuskanshi tace "da gaske?" Gyadamata kai yayi yace "eh" ijiyan zuciya Mama ta sauke tace "to inane gidansu yarinyar naje na bada hakuri" ahankali yana sakin knees nata yace "basai kin bada ba lafiyanta kalau Mama, is just normal misunderstanding da kananun maganan yara yajawo fadan kada ki damu kinji" gyadamai kai tayi tace "Allah maka albarka" murmushi yamata kadan baice komiba, Mama tace "bari natafi gida to Alhamdulillah nagode nagode nagode kaji" daga yanda take maganan kasan hankalinta ya kwanta gyadamata kai yayi, Mama tace "to sai an jima" "saida safe Mama" yafadi ahankali, Mama ta wuce cike da farin ciki tafara tafiya kadan kadan sabida yanda kanta ke sarawa, tayi tafiya daya biyu uku ana hudu kawai ta yanke jiki tafadi, Riyad na tsaye yanama security magana sukaji karan fadin abu juyowa sukayi ganin Mama yasa dawani irin gudu Riyad yayi wajenta suma security din haka dago kanta yayi yana tapping hannunta yana kiranta. "Mama Mama Mama" amman shiru dasauri yace "help me" daukanta sukayi yabude bayan motanshi yasata yakoma yashiga gaba yatada motar sai wani babban private hospital dayake zuwa anytime yake Kano yana zuwa aka karbi Mama sai emergency yawuce office na Dr dinshi ya shiga Dr ya sallami patient dayake tareda shi yace "Ranka shi dade mai Martaba" dan yatsine fuska yayi yace "don't call me that I have a patient tana Emergency I want you to be on her case fast" tashi Dr yayi suka fito tare ya shiga emergency din, shi ya tsaya agaban wajen yarasa yanda zaiyi sai kuma yakoma office na Dr ya zauna, yana nan zaune yana jiranshi har aka kira magrib saiya tashi yafito yawuce mosque yana gani Munir na kiranshi yaki dauka salla yayi yafito yawuce ciki yakoma office na Dr yazauna sai gashi Dr yashigo dasauri Riyad yatashi yace "how is she ta farfado?" Gyadamai kai Dr yayi yace "da kyar muka samu ta farfado amman tana bacci" saikuma ya zauna ya kalli Riyad yace "kasan wacce ka kawo? Who is she to you?" Batare daya amsashi ba yace "does that matter? Meke damunta? How can I help?" Gyara zama Dr yayi yace "she's HIV patient!" Yayi maganan yana kallon fuskan Riyad dayaga bai chanza ba saima yace "me da me take bukata yanzu"? Ahankali Dr yace "is like she's on medication so bahsine abinda ke damunta ba bashine kuma dalilin yankewan jikinta tafadi ba, abinda yafi komi damunta is BP, BP ta yayi raising sama sosai I don't think zan sallameta yau ko gobe ko jibi ma sef, sai ya sauko sannan zan sallameta, just get wanda zai zauna da ita and then drugs" yashiga rubuce rubuce duk

Riyad na kallonshi saida yagama komi sannan yanunamai takardan, tashi Riyad yayi yazaro wallet dinshi ya ijiye akan table din cikeda izza yace “take any amount kake bukata for drugs, bills, pin is 6648” yana maganan yawuce yafita akasaitance yasauka kasa dakin dayaga an shiga da ita yawuce shiga yayi ahankali ya tsaya bakin gadon an cire hijabinta daga ita sai riga da zani da hulan dake kanta an samata drip, shiru yayi yana kallonta sannan yajuya yafice daga dakin yawuce yaje motanshi yashiga yadau wayanshi yana shirin kiran Munir wayanshi yashiga ringing Munir dinne yana dagawa kafin yayi magana yace “Munir open file na employees dina a desktop get info na Rashida I need address nata ASAP” kafin yayi magana ya katse wayan yayi shiru chan saiga Munir din yakira yace “suna Ranji, wajen tudun Murtala” baimasan inane wajen ba but haka ya katse wayan ya kunna google map yashiga driving….

Tunda tai magrib ta zauna tai shiru tana mamakin ina mama taje harta dau hijabi kota bita hotel dinne ko wani case dinne akeyi achan but karta kara bata ran Mama taje wajen hakan yasa ta daure ta hakura, kuma zai iya yuwa tadawo takai karanta wajen Baba liman ne dantana haka wani zubin hakan yasa ta zauna adaki zugum kaman wata marainiya idan aka kira isha’i bata dawo ba zatasa Hijabi taje ta nemeta….

Shigowa layin yayi ga majalissar maza gaban shaguna ana zance rage wutan motan yayi karya haskosu yana karasowa yakashe motan kawai ya bude ya sauko yazo wajen yamika musu hannu yace “Assalamu Alaykum” atare duk suka amsashi suna karban hannunshi ganin arniyan motan dayake ja, yace “dan Allah tambaya nake” dasauri sukace “Allah sa mun sani” anatse yace “gidansu Rashida nake nema” tsit wajen sukayi kaman ba su ba saikuma daya daga cikin samarin yatashi yace “bismillah yallabai zomu kebe mana” binshi Riyad yayi sujkaje wajen mota kaman mutumin arziki yace “nasan ba laifinka bane Rashida kam nada kyau Masha Allah yarinya kaman Balarabiya amma dai kyan dan maciji ne, yanda muke gayamaka dinnan haka muke gayama duk wani saurayi dazaice zaizo nemanta hakkinmu ne na yan unguwa, hakkin makotaka tunda su basu fadin gaskiya” tunda yafara magana Riyad yaji ranshi na baci amman ya daure dan he wants the address, mutumin yace “kagadai uwar yarinyar nan fasika ce garin kwashe kasheta ta kwaso kanjamau Rashidan ma muna kyautata zato tanada shi tun acikinta tasam….” “Zaka fadamin adreshin ko bazaka fadi ba”? Riyad tafadi sounding bitter and angry baki mutumin yabude zaiyi magana Adamu mai chemist da tun zuwan Riyad ya hangoshi daga chemist yace “kaje chan kasan layi zakaga gida mai jan kofa nan ne gidansu Rashida” kallonshi Riyad yayi yace “thank you” yawuce yakoma mota yatada mota yabar wajen, gaban gida mai red door yayi parking ya sauka ya tsaya gaban kofan yakai hannu yayi knocking, Rashida na zaune kan dadduma taji ana knocking hakan yasa ta tashi dasauri batare data cire pink hijab dinta ba tafito silipas ta zura gabanta sai faduwa yake ta taho zaure tana mamaki Mama ta kulle kofan ne dazu dan idan aka rufe yana shiga jam, ganin kofan abude ga wani arnen black car parked agaban gidansu wani mutumi a tsaye yajuyama kofan baya so bata ganin fuskanshi yasa ta fito kai tsaye cikin muryanta mai bala’in dadi tace tace “kaine kai knocking wa kake

nema?” Har cikin zuciyanshi yaji sanyin muryanta hakanan, cikeda wani irin kwarjini yajuyo yana zuba hannun cikin aljihun rigan dake jikinshi, hada ido sukayi ta kalleshi ido cikin ido dan akwai wuta a kofar gidansu mamaki da tunani yacika kanta, ba mutumin nan bane mai hotel dinda take aiki ba? Ko idanunta gizo yake mata? How is he agidan su? Ganin ya tsaya yana kallonta bayako kyafta ido yasa tadan dauke kai tattare bakin hijabinta tashigayi tana tabawa saikuma takai hijabin bakinta, saichan tacire, saikuma chan ciki ciki kaman an sata dole ahankali tace “ina yini” he’s looking at her mostly sabida baisan mezai fada mata ba, chan yace “Mama wants to see you” hakanan gabanta yayi bala’in fadi dasauri ta kalleshi baki tabude zatai magana saita kasa sabida yanda kirjinta ke bugawa da gudu da sauri sai kawai ta tsugunna, wani irin tausayi yaji tabashi yakasa cemata komi, da kyar kusan 30sec sannna ta mike jin tadawo daidai cikeda karfin hali tace “ina Mama wat happened to her? Nace mata kartazo tabada hakuri but taki jina, normal Mama da tuni tadawo, tana ina yanzu? Just tell me wat happened to my mother mekuka mata? Me kuka gaya mata? My Mom is very sick, tell me tana ina yanzu?” Tai maganan hawaye na cika idanunta harwani kyalli suke adake still kallonta yake yace “she’s fine now but tana hospital” hannuwanta biyu ta daura a fuska saikuma ta juya takai hijabinta ta goge fuskanta tass tajuyo ta kalleshi da jajayen idanun hijabinta daya jike da kuka ya kalla sannan yakalleta, cikeda dauriya da karfin hali tace “inane asibitin bani address din natafi” batare dayay magana ba yajuya yace “get few things da Mama zata bukata lock the house I will take you there is late bazakije da kanki ba” yayi maganan authoritatively yawuce yabude motan ya shiga gaba, kallonshi tayi sai hawaye sai kawai tajuya takoma cikin gida, drawer tabude takwaso simple t-shirt tasa ajaka tadaga kayansu ta dauko ledan duka kudin dasuke ijiya 139k, tadauki dadduma da zanin gado wankakke tasa ajakan bayanta takashe wuta tafito sai goge hawayenta take tarufo kofan waje tasa key sannan tajuyo ta kalli motan, bata taba shiga mota babba haka ba, ahankali yakawo hannunshi yabude kofan ganin yanda take kallon motan kaman matsoraciya, daurewa tayi ta matso ta shigo ta zauna agaban ta maida kofan tarufe wani sanyi da kamshi na dukanta ta rungume jakan a hannunta gam.

Mama na duke a tsakiyan anguwa tana kuka sosai ana kallonta an taru Hajiya Jummai tazo inda take tsugunnawa tayi takai bakinta saitin kunnen Mama tace “mission accomplished! Now watch how I will ruin rayuwar yarki this is just the 1st step, watch and see how zanyi feeding yarki to those hungry police officers, I will make sure sunyi kacha kacha da duk wani abu daya maidata diya mace, barima kiji Amarya na aikamusu yau akwai biki” tawani kwashe da dariya, juyo da kanta Mama tayi ta kalleta irin kallon nan na bakomi akwai Allah sannan tace “nabaki raina ki dauka Jummai, yau kidauki wuka ki sakamin aciki na mutu na yarda, kome kikeso kiyi dani kiyi amman spare yarinya na, she’s a small girl, meta miki? Mijinki dama tun tana ciki yace ba tasa bace haryau ko fuskanta baitaba ganiba to meta miki? She’s not a threat, she’s a small child kulleta a police station will ruin her life, Hajiya Jummai banda kowa sai ita, kiyafema Rashida ni kisa a kulleni” murmushi tayi tace “kinga I hate you with every blood na jikina saisa I want to end you using abinda kikafi komi so, wlh wlh ko kudina zasu kare yau saina tabbatar an yaga yarki a cell, wlh sainasa sun maidata nama, saina tabbatar sun halakar da rayuwanta tass, maybe then na hakura nasa afito da ita kokuma na aikata prison she need to be taught a lesson, ke I will cook her up bazata fito daga cell anytime soon ba, this is for auren Mijina dakikayi!” Tana maganan ta tashi tawuce wajen mota ahankali Mama tajuyo da rinannun idanunta ta kalleta ga mamakin Mama saitaga yan matan sun taso fess da kafansu sun fito sun shiga mota direba sun yatada motan sun tafi, Ahankali Mama ta tashi wani kalan bubbugawa zuciyanta keyi dabai taba mata arayuwanta ba, yan layin sai kallonta suke mata an lalleko daga gida tanaji ana kananun magana ana dama maraji makomarsa kenan anzo baku abinci mu makota mun shaida but yarki tazo tana dukan mutanen arziki ai gashinan tahadu da daidai da ita, gida Mama ta shiga ta tattaro duka kudin dasuke dashi tasan belin mutum da kudi akeyi sunada 80k agida a account din Rashida kuma akwai 100k da aka mata salary na hotel just jiya 50k ake biyanta but sallan nan sai aka basu 100k, sakawa tayi a lalita tasa takalmi tafito ta kulle gidan ta shiga tafiya bama tasan wani police station aka kaita ba, tafiya take a anguwa wasu nacemata Allah kiyaye gaba wasu na Binta da kallo Adamu me chemist ne yafito hangota dayayi dan shi yana mutunci dasu yace “Mama Allah kiyaye gaba ina zaki yanzu”? Bama ta iya magana sai hawaye bakin hijabinta tasa tace “bansani ba duk police station dana gani zan shiga” dasauri yace “ina ganin kije head quarter dan naga babban police car suka zo dashi sabida local street police post ba’a ijiye musu manyan motoci haka, Allah kiyaye gaba” gyadamai kai tayi ta wuce ta tare keke ta shiga 500 aka kaita headquarters.
Sauka tayi tashiga ciki ta tafi chan gaban kanta yan sanda dake wajen sukace “lafiya Hajiya” baki Mama tabude zatai magana sai kuka matar tace “Hajiya dan Allah kifita ki gama kukan saiki dawo” dasauri dayan dan sandan yace “mehaka Grace? Mama lafiya calm down meya faru fadamana”? Da kyar ta tsagaita kukan tace “y’ata wasu yan sanda suka kama kusan minti talatin kenan bansan inda aka kaitaba yan anguwan mu since nazo nan headquarter” mutumin yace “ya sunan diyar taki”? Ahankali tace “Rashida Almustapha” log book dake gabansu yaduba yaga sunanta kafin yayi magana Grace tace “banan aka kawota ba kije wani police station din” kallon Matan Mama tayi saikuma ta kalli wanda ke attending to her ahankali yace “Mama je waje ki zauna ina zuwa” fita waje Mama tayi tasami waje ta zauna, kirjinta bugawa yake like never before ga azumi abakinta wlh kusan 2hrs tai spending awajen dan har 5 tayi sannan yafito yazo wajenta yace “zo gefe Mama” Dasauri Mama tabishi ahankali yace “Mama

bansanki ba amman kin bani tausayi wlh tuntuni sai bin office daban daban nake ama barki kiga diyarki sunki, wai yaran data daka suna ICU, sannan she attacked officer mu wata and abuse her" cikeda tashin hankali Mama tace "wlh wlh karyane sherine agabana yaran suna shiga mota da kafansu basa ICU, kuma wlh Rashida bata taba police dinba" ahankali yace "to yanzu dai bani dubu goma zan taimakeki da kyau koda yarki zata kwana zansa ido akanta kar acutar da ita" fashewa da kuka Mama tayi tana tura hannu alalita ta kirgo 10k tabashi ya karba yace "bari kiji Mama the truth is powerful mutane sukasa aka kulle miki yarinya dan haka yanzu dai idan kinada wani babba haka kije kitaho dashi ko za'a miki alfarma abaki belinta inba hakaba wlh bazama kisan yarki na nan ba ninedai nafada miki" yanda Mama ke kuka sai yataba zuciyanka tace "wanake dashi? Banda kowa sai Allah ni" dan sandan yace "nidai nayi miki iya nawa kije ko waye kisamo, suna ganin kalan kudi ajikinsa zasu badata, bari nakoma ciki kada anemeni" wucewa yayi yakoma ciki yabar Mama wajen tsaye shiru Mama tayi saikuma ta daga idanunta takalli sama irin kallon Ya Allah kana ganin komeke faruwa sannan tasa bakin hijabinta tashiga tafiya tawuce gate kafanta yayi butu butu da hijabinta ma sabida zaman kasa datayi sai tunani take ina zata shagon Mama miwa tane tunda tanada kudi but tace baruwanta da police station bata zuwa, Rashida tafada mata tace taji ance Riyad na Umara saisa batai tunaninsa ba.

Bari taje ta gwada yima manager magana kozata taimaketa gashi Baba Liman yaje kauyensu shima duba gona, adaidaita tasake shiga ta tafi hotel din hanyar shiga taje yauma wasu security daban ne dana ranan suna ganinta sukace "ina zaki"? Arude Mama tace "manager zan gani" wani kallo suka mata daga sama har kasa sannan sukace jira anan daya yashiga ciki yama manager magana tafito daga office nata hango Mama tayi daga glass door tace "I don't know her, please send her away yau banda lokacin all this beggars I'm very busy" takoma office security yafita yaje inda Mama take tsaye yace "batanan" tsayawa Mama tayi tana kallonshi yanda taji kaman jiri na neman dibanta batasan sanda ta duka ba saitahau kiran sunan Allah. "Allahumma ajirni fi musibati……Innalillahi wa innailaihi raji'un, Ya Allah kadubi yarinyana dake cikin cell kar awani abu yasameta please karsu cimma burinsu" tashi tayi tana taba bango kawai kaman kanta ya kwance takeji cus batada hope kuma yanzu sai magana take ita kadai. "Rashida na is scared, yarinyana bata taba zuwa police station bama, yanzu tanachan locked up a cell an ciremata slippers, an karbe komi nata, hala ana azabtar da itama, idan suka batama mata rayuwa fa, wat if they rape her? My poor baby must be so scared yanzu, yarinyana batada kowa aduniya sai ni, wat are they doing to my child right now………." Diiiiiiiiiiiiii! Taji karan ana daddanna mata car horn dayasa kawai ta birkice hannunuwanta tadaura saman kunne ta kulle idanunta kawai tahau juwajuwa akan titi go slow kawai yahadu bama tasan meke faruwa ba, "Mamaa!" Taji an kira sunanta da karfi dasauri tabude idanunta dasukai jazur, Riyad tagani tsaye agabanta yana sanye da farin shadda datasha aiki kanshi da kula ganinshi kawai saita fashe da kuka sosai ahankali yasa hannunshi yasauke hannayenta daga saman kunne ganin she's not herself yakama hannuwanta duka biyun sukabar tsakiyan titi zuwa motanshi yabude baya yasata shima yashiga bayan wani bodyguard dake tukanshi yaja motan suka gangara gefen hanya yayi parking, Riyad dake kallonta yace "Mama menene? Why are you in the middle of road"? Bakinta rawa yake ta birkice kawai tace "Riyad…….Riyad…….Riyad" hannunta yakama ahankali yace "get me water" fita direban yayi anatse Riyad yace "Mama calm down I'm here now, calm down everything will be fine, calm

down Mama kinji" bakinta is still calling name nashi, ahankali yace kice "Innalillahi Wa Innailaihi Raji'un" ahankali Mama tace "Innalillahi wa innailaihi raji'un" dan natsuwa tasamu kadan daidai lokacin an kawo ruwan budewa yayi yabata tasha kadan sannan yace "wat happen Mama"? Fashewa da kuka tayi tace "tasa an kamamin yarinya an kulle a police station" anatse yace "wace"? "Kishiyata wacce mukai zaman aure tare kafin mijinmu ya koreni"? "Wat happened Mama"? Labari Mama tabashi tundaga time datazo gidan da time da Rashida ta shigo, da all abinda yafaru da duka abinda tagayama Mama na zatai feeding Rashida to yan sanda" jiyayi ranshi yayi tsananin baci, "drive" yafadi ahankali yama Munir text dan daga gidansu zuwa head quarter is even closer than daga nan hotel zuwa wajen.

Wajajen magrib sukakai police headquarter ya kalli Mama yace "Mama ki zauna anan zan fito da ita kinji" gyadamai kai Mama tayi ya kalli security yace "make sure she stays in the car she's not feeling well" "yes sir" ya amsa yana fita yaga Munir yafito daga tashi motar ga sauran bodyguard nashi yayi gaba kawai Munir da guards nashi na binshi abaya, all eyes yadawo on them ko kallon yan sandan wajen baiyiba yawuce sama direct zuwa office na inspector cus yasanshi sosai yana kawo gaisuwa fada dudda bai sanshi babu rawani ba, kai tsaye yabude kofan ba knocking babu komi Inspector na zaune yana dube duba, da zafi sosai an anger kan muryan Riyad yace "I will sue you and I will sue the entire police headquarters for rashin adalci for tauye hakkin talaka, for rashin yin investigation, I will make sure anyi sacking all of you anyi replacing naku with better and eloquent officers dasuka shirya yin aikinsu yanda yakamata" from yanda yake magana kadai yasa gaban Inspector yashiga faduwa yama kasa magana, Munir yace "you must be confuse kana magana da Mai Martaba SARKI RIYAD! Sarki mai adalci, sarkin talakawa" wani kalan tashi inspector yace "an gaida Mai Martaba Allah huci zuciya ka, tub……" hannu Riyad yadagamai yace "release Miss Rashida Almustapha, and nabaka 24hrs kuyi realeasing evidence cewa yaran data daka suna ICU with Doctors report and everything, and again inaso kuyi proving cewa she's really a killer, banda haka I want to know wat right that officer takedashi to slap and hit Miss Rashida, and again wanda aka bishi har gida shine akaje neman tsokana, prove all this ba set up bane inba hakaba" Munir yace "zaku hadu da bacin ran Mai Martaba" baki Inspector yabude zaiyi magana Riyad yadagamai hannu for the second time yadakamai tsawa sabida yanda ranshi yake abace yace "release her now!!!!" Shi kanshi Munir saida ya kalli Riyad rabon dayaga dan uwanshi yayi fushi haka harya manta, da wuya Riyad yayi fushi, jikinshi har rawa Inspector yake yafita dasauri shi baimasan case din ba duk suka bishi yawuce kasa Riyad na biyedashi yadauki key na kofan da ake budewa a shiga bangaren cell nasu yabude kofan da sauri ya shiga saikuma ya juyo yace "Allah taimaki ranka shi dade ban santa ba ita yarinyar" wuceshi Riyad yayi kawai yashiga ciki mutumin ya bishi abaya cell cell ne daban daban, na mata daban na maza daban but duka ajere suke, ga mutane kukkule amman baiga Rashida ba in any of cell na mata dasuka wuce ba, zagawa dashi Inspector yayi zuwa cell masu kama dana kaji ana kiran dakunan NO SS CELL wato no sitting no standing cell, wanda shi na punishment ne bazaka iya tsayuwa ba bazaka iya zama ba kana duke kawai idan anaso a azabtar dakai ake kaika wajen, hangota Riyad yayi ita kadai an rufeta a cell dayakenan kaman cell din dan buri alalo alalo gwanin ban tausayi she looks very very miserable and terrible ko kadan bata kallo inda suke ba danta dauka matarce tadawo, ahankali Inspector da gabanshi ke faduwa ganin ita kadai ce abarayin NO SS yace "itace naga kana kallonta"?

Juyo da kanta Rasheeda tayi jin datayi anyi magana tunda ta shigo wajen sai yanzu taga haske hasken Riyad dake tsaye yana kallonta idanunshi sun chanza launi kallo yake mata dabazaka iya tantance na menene ba, ahankali yake kallonta even though she’s not crying but kasan she’s very very scared, she’s terrified, she’s lonely, she’s afraid, dauke kanta tayi daga kallonshi da sauri tashiga wasa da fingers nata, bude kofan Inspector yayi yace “fito” kokarin motsi tayi da kafa amman takasa sabida yanda kafafunta suka sankare suka rike sai kawai Riyad yaji zuciyanshi ta tsinke awani irin hankali yafara tafiya dudda bata kallonshi but every step nashi tana jinshi har a bangon zuciyanta, ahankali azo gaban cell din ya tsaya chak still taki dago da kanta, yakai wajen 10secs yana kallonta kafin awani irin hankali yaciro hannunshi daga aljihu yamika mata cikin wani irin murya mai masifan taushi yace “Rasheedah!” Har kasan zuciyanta taji yanda yakirata hakan yasa tadago kanta takalleshi sannan takalli hannunshi dayake mika mata batare data karbi hannunba, ahankali yace “come Mama is waiting” dasauri ta kalli fuskanshi kafin awani irin hankali takai hannunta tadaura gently kaman mai tsoro cikin nashi, atare dukansu sukaji shock amman yadaure yakamata sannan ya fizgota tashi daya tafado kirjinshi making deep sound mara kara sosai dazai nuna how hurt she’s, kafafun na mata ciwo sosai amman sabida dauriya da taurin rai taki nunawa but takasa motsi tana kirjinshi, dan sauke kai Inspector yayi aranshi yace “budurwan mai martaba muka kulle dama? Suwaye keson sani a bala’i” takai one minute a kirjinshi batare daya taba bayanta ba banda hannunta daya rike but ita takasa motsa kafan tafita daga kirjinshi, in a very caring tone dabama tasan yanada shi ba yace “can you walk now”? Duk yanda taso karta kalleshi kasawa tayi tana kirjinshi tadaga fuskanta takalleshi hada idanu sukayi cikeda tsananin kulawa yace “can you walk yanzu?” Very soft itama ta gyadamai kai tana yunkurin fita daga kirjinshi, saitai baya zata fadi dasauri yakai hannunshi daya yakama waist nata sai kawai adake yakama hannunta daya yakai ta bayan kanshi ya ijiye yayi supporting nata dakyau kafin yace “let’s go” she’s scared internally, she’s shaking bamata da karfin wani abu so she just followed him tana dan dingishi suka fito ahaka.

Hannu yasa yabude kofa mutanen data gani awajan da yawa gasu police gawasu kaman bodyguard ga Munir datake gani a hotel nasu ga yan sanda maza biyu na dazu bataga macen ba yasa tadan yunkura cikeda karfin hali zata fita daga jikinshi kaman daga sama taji saukan hannunshi akan waist nata yamaidata side nashi da kyau dawani irin sauri tadan juyo da kanta ta kalleshi but fuskanshi is looking straight bayako kallonta yacigaba da tafiya da ita hakan yasa ahankali ta maida kanta kasa daidai sunzo kofan fita saiga yar sandan dazu tana shigowa itama suka hada ido wani abu Rashida taji yazo mata wuya ya tsaya duk kalan ciwon da kafanta ke mata amman saida taji tasami karfin daga kafan kawai takai ta kwasheta within a blink of an eye jikake tippptipp! Officer tai wani mummunan faduwa danko ita bata lura da kafan da Rashida tasamata ba dan fuskan Rashidan take kallo dana Riyad datagani tareda ita, da all the people dake wajen,  yan sandan sukai kanta ganin kalan faduwan datayi ana “lafiya kika fadi haka sannu me kike kallo haka” dan babu wanda ya lura da abinda Rashida tayi dagowa officer tayi hancinta na jini ta kallo kofan hada ido tayi da Rashida dake mata kallon munyi settling score dake, tsayawa shima Riyad yayi yana kallon Rashidan cus he saw wat she did saikuma kawai yacigaba da tafiya da ita suka fice har wajen motan shi su Munir suka biyosu baya yabude baya Mama idanunta harsun kumbura na zaune taganshi da Rashida dataga har yar rama tayi, sai kawai Mama tafashe da kuka jikin Rashida yayi mugun sanyi da taimakonshi ta shiga bayan

motan sai kawai ta rungume Mama dan jim yayi yana kallonsu kafin ya maida kofan bayan yarufe yajuyo yadan taka zuwa wajensu Munir dake kallonshi kallon what is going on, anatse yace “I will see you at home bari na kaisu gida” bai jira amsan Munir ba yajuya yawuce saiya shiga gaba direban yatada motan yaja har lokacin Mama kuka take wlh takasa magana ma, hakuri take ta bama Mama amman yana shigowa tayi shiru kawai dai ta rungumeta agaban wani pharmacy yasa aka tsaya yafita yashiga yakai kusan 10min aciki yafito rikeda leda yadawo ciki ya zauna aka tada motan har zuwa anguwan su parking yayi yabude gaban motan yafito yabude bangaren Mama ahankali Rashida tasaketa goge fuskanta tayi ta sauko sannan ta mikama Rashidan hannu tace “taho muje” cike da karfin hali ganin yana wajen yasa tace “ni zan iya fita dakaina” tsayawa Mama tayi tana kallonta irin kallon wani irin taurin kai da karfin hali Rashida kedashi ne, shima Riyad folding hannunshi yayi a kirji ya tsaya kawai suna kallonta jan jiki tayi har tazo bakin kofan ahankali ta daga kafa daya tafito hakama dayan sannan ta yunkura ta tashi dudda she’s not showing the pain a fuskanta but wlh kasan da kyar take komi takawa tashigayi ahankali sai kawai tawuce tai zaure da dafa bango ta shige cikin gida, Mama tabiyota abaya tana shiga rabin buhun shinkafar taci karo dashi a tsakar gidan nasu jitayi zuciyanta kawai yarikice ranta yabaci tama manta tanada ciwo kawai tai wajen shinkafan azuciye ta daga shinkafan zata mike kafanta yayi wani irin kara da duk dauriyanta saida tai ihu daidai lokacin Riyad ya shigo gidan azuciye yayi wajen yasa hannu ya fizge buhun shinkafan yayi ihu yace “what is your problem?” Kallonshi tayi ido cikin ido tace “mezamuyi da shinkafarsu? Zubarwa zany…….” “Quiet!” Riyad ya daka mata tsawa da saida taji jikinta yayi rawa, cikin tsananin fushi ya nuna Mama datake rabe a bangon zaure kawai ta tsaya chak tana kallon yarinyar tata gwanin ban tausayi, irin kallon yaya zanyi da wannan yarinyar ya Allah, yace “can you give your Mom just a minute of peace?” Kallon Mama tayi saikuma ta kalleshi zata bude baki authoritatively Riyad yace “I said quiet!” Cikin kwayar idanunshi ta kalla the anger datake gani da fushi kawai saitaji takasa magana wani bai taba shutting nata up in her life ba sai yau, cikeda tsananin bacin rai yace “kina tunanin komi arayuwan nan you settle it da fada da duka you think is by fighting?” Yasake shiru saikuma ya lumshe idanu tareda fuzar da iska yasake kallonta yace “every action have consequences do you for once sit down kiyi tunanin waye ke suffering consequences na action naki?” Yadan mata ihu kadan still kallonshi take da manyan idanun nan nata, saiya sake nuna Mama dake tsaye looking at them tana goge hawaye da bayan hijabi yace “do you have slight idea of abinda Mamanki went through today? Did you even know an ina naganta?” Yasakeyin shiru saikuma a sanyaye yet da tsaurin harshe yace “do you even love your mother?” Wani kallo datamai har saida idanunta sukahau sparking sabida anger kaman zata rufeshi da duka, cikin fushi tace “kai waye dazaka tambayeni ko inason mahaifiyata, waye kai”? Cikin tsatsauran murya Mama tace “tamaka rashin kunya ka yanka mata mari Riyad!”.

RASHIDA IS STUBBORN CUS WATT🔥
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE2️⃣1️⃣

BARI NA LISSAFO MUKU ABUBUWAN DA HABISHMA UNDERWEARS KE SAIDAWA💃
Pants(cotton, seamless, lace, spandex, plus size,thongs, gstrings etc),

Bras(nursing, padded, non padded, uk, wired, wireless, seamless, t-shirt bras, plus sizes etc)

Tights(long, short, leggings, bumshorts, laser cut tights, jeans etc)
Underskirts(silk, cotton, long, short, box, plain etc)

Sleepwears(pyjamas, adult and children pyjamas, long sleeve, short sleeve, long trousers, short trousers, dresses/gowns, character sleepwears, erotic sleepwears, enchanting sleepwears, long gowns, maternity gowns etc)

Boxers(men, boys, women, girls etc)

Vest(men, women, boys, girls etc)

Tops(chiffon tops, thick cotton tops, body hugs,  etc)

Long camisoles, innercaps(plain, ribbed and chantilly), deodorant powder that guarantees 48hrs protection
CHAT THEM UP TODAY A WATSAPP KISAI NAKI💃
+2349034049623
+2348064643886
Kallon Mama Rashida tayi zuciyanta yafara tsinkewa ganin shi Mama take supporting tabude baki zatai magana saitaji kuka na son subuce mata hakan yasa tarike maganan da kyar ta danne kukan tace “to sai in tsaya ina kallo ana zagin Mamana”? Rai abace Riyad yasa hannu a lips nashi yace “shush” abu taji yazo mata wuya wayeshi dahar zai dinga mata fada agidansu kuma Mama na supporting nashi sai kace wani Yayanta, dauke kai tayi daga kallonshi tana huci kaman damusa yace “zagi baya kari, zagi baya chanza fatan mutum, you are a very selfish girl that care about feelings nata not her mother” wannan karan juyo da kanta tayi ta kalleshi idanunta sun ciko da hawaye amman tahanasu zubowa shima yana kallonta kyar yace “duk yaron daya gwammace yabi zuciyanshi dayabi maganan Mamanshi is selfish! Your mother is sick! Anything daya shafeki affects her greatly, akanme bazakiyi hakuri ba just for her safety and wellbeing huhh? And kince kinason Maman ki? Your are just a terrible selfish daughter wacce ta damu da ego nata not her mother” shima yayi maganan idanunsa na ja Mama kawai kallonsu take bata tabajin tanason Riyad kaman yanda taji tana sonshi ba yau, cikin fushi yace “your Mom nada BP very high BP, kwanciyan hankali takeso but kullum cikin tashin hankali take sabida ke! Kullum fitinan ta kike da fitinu daban daban do you want to kill her?” Daidainan

hawaye ya zubo sharr daga idanunta da sauri ta dauke kanta tasa bayan hannu ta share, cikeda fada yace “I saw your Mom at the middle of titi bamatasan metakeyi ba she was panicking calling your name, yarinyana! Y’ata, da kinfito daga police station kinga ta mutu fa?” Takawa yayi zuwa inda take facing ya tsaya chak agabanta adake hakan yasa ta kalleshi da rinannun idanunta ya nuna mata yatsu cikeda wulakanci 👉🏻 yace “take this as your last and final warning, idan kika kara troubling Mama zanzo I will take her away from you na kaita inda za’ayi cherishing nata forever, sannan abata peace of mind data rasa daga wajenki, I dare you ki kara trying wani nonsense hali dazai tadama Maman ki hankali saina sabamiki you selfish egotistic girl!!” Yana maganan yajuya zuwa inda Mama take a zaure cikeda so yace “muje Mama” juyo da kanta tayi ta kallesu abunda taji tuntuni yana wuyanta kawai taji yazo mata baki da sauri tajuya tashiga daki tawuce uwardaka sai kuka taji kawai ta tsani Riyad, kishi yakamata yanda Mama kaman tafisonshi sama da ita, he’s making her look like a bad daughter.

Zaunar da Mama yayi akan tabarma sai ya zauna a gefenta yace “Mama kidena damuwa kinji she’s fine babu abinda yasameta, itakuma Matan zansa anemota she will pay for abinda ta muku” dasauri Mama ta girgizamai kai tace “Riyad tunda ka karbomin Rashida kabar mutanen nan da halinsu duk inda kake tunani sun wuce haka I don’t want to involve you a matsalanmu this people are terrible and very powerful banso sumaka wani abu, kamin alkawari bazakasa anemota ba, kabarta da halinta, karma ka koma police station din, bawai koda yaushe take damunmu ba, rabonta da gidan nan kusan 5yrs ago sai yau datazo maybe sai nan da another 5yrs kuma zata kara zuwa, banson wani tashin hankalin banson damuwa, banda ma karfin zuwa police station bada statement, haka kuma banso Rashida taje police station wazai aureta? It will ruin her life? Cell din nan kadai yanzu ma yayi ruining life nata yan anguwan nan babu inda bazasukai labarin ba, I’m tired of all this, I keep causing pain arayuwanta, nice darkness na rayuwanta, nasan Rashida bataji she’s stubborn but she became like this sabida ni, no body wants to be friends da ita, no body wants to marry her, koyaya wani yazo nemanta Sheri da gaskiya sai yan layin nan sun tara sun fada akanta yanzu kuma dataje cell we are ruin gabaki daya” Mama ta share kwallan daya zubomata saikuma tadaga kai ta kalli Riyad da fuskanshi yayi kaman zaiyi kuka tace “Riyad kamin komi arayuwan nan wanda har dan uwana na jini bemin ba, thank you for everything, thank you for saving my daughter’s life, nagode Riyad kaji, but don’t involve kanka in our personal family issues is not worth it, babu amfanin shiga 23yrs of matsala kana shiga zata dawo sabuwa I hope you understand”? Shiru yayi sai chan ya gyadama Mama kai yace “I understand Mama nabar case din but duk randa tasake zuwa I won’t spare her” murmushi Mama tamai tace “tashi kaje gida kaima ka huta gobe salla, kasha ruwa Allah maka Albarka” wlh har cikin ranshi he’s feeling very attached to Mama kaman karya barta ahaka amman yadaure ledan Pharmacy dake aljihunshi yaciro yabata yace “gashi Mama na kafanta ne” yayi maganan yana tashi yace “saida safe Mama” kallonshi kawai Mama take cikeda kauna tace “saida safe Riyad ayi salla lafiya” sannan takalli ledan pharmacy din tana tuna yanda yama Rashida fada yanzun nan saikuma tai murmushi.

Gyara zama Mama tayi tai shiru ita kadai awajen Allah kadai yasan tunani tunanin metake bini bini tasa hannu ta share hawayenta dayake zubomata, ruwan dabatasha kenan ba, har wajen

12 na dare ita kadai, sannan ta tashi da kyar tawuce tayo alwala kanta kaman zai cire tashiga daki tadauki pure water tasha sannan tahau dadduma azaune tai sallan tana idarwa tashiga uwardaka akasa taga Rashida na bacci ko hijabi bata cireba tsabagen fitina, zama tayi wajen ta yaye skirt na jikinta tadauki ledan ta ciro man shafawan daya siyo Mama tai shiru tana kallo saikuma ta kalli fuskan Rashidan ahankali tace “stop this madness and see Riyad Rashida, is because you’re hurt abin yakara batamai rai yake miki fada not just sabida ni kadai” dan murmushi kadan Mama tayi tace “he’s romantic” saikuma takai hannunta saman bakinta kaman mainin kunya tace “ke Zainabu” budewa tayi ta lakato ta shafa mata maganin a kafafunta sannan ta ijiye maganin saikuma tai tagumi tana kallonta addu’a kawai take Allah yarage mata zafin zuciya da yawan fushi din nan kar watarana fushi yasa tai kisan kai yanda ta watsar da matan nan biyu dazu ga jini a goshinsu Mama ta girgiza ainun batasan Rashida tayi nisa hakaba.

Har asuba tayi Mama bata kulle idanu da sunan bacci ba.

Ahankali tabude idanunta jin an tabata ganin Mama sanye da hijabi tai alwala yasa ta tashi zaune da sauri ahankali tace “Mama” kallonta Mama tayi saitai shiru bata amsaba kaman irin da abin ta kwana hakan yasa tafashe da kuka mai karfi tace “Mama dan Allah kiyakuri ki yafemin bazan kara miki rashin ji ba, kome kikace nayi zanyi, Mama everything is my fault, danaji maganan ki dakikace nabari nabarsu munshiga dakin da duk haka bai faru ba, Mama da mota ya kadeki dame zan gayama Allah”? Yanda take kuka wlh saita baka tausayi Mama taso yau ta shareta Amman saitaji bazata iyaba saita zauna tace “kimin shiru” tsagaita kukan tayi tana kallon Mama da rinannun idanunta, ahankali Mama tace “yawan fushi nasa kai abu da dama dazakai nadama Doctor” cikin raunin murya tace “Mama u hate that woman, I hate mijinta, I hate entire family nasu, those people made you suffer all your life har yanzu kuma basu barkıba” Mama na kallonta tace “idan zaki bimin hakki na ne then kiyi focusing a school, ki gama school ki zama wani abu, ki nuna musu cewa Mamanki dasuka wulakanta ta haifoki diya me albarka me goshi, ki zama Dr tukunna and cure me kinji kidena fada da mutane akaina focus on goal naki nan gaba na warke no body can troll me right”? Gyadama Mama kai tayi Mama tace “bansan ko zamuyi rayuwa tare har karshe ba babu wanda yasan gobe ke babu wanda yasan anjima ma, idan bana raye kikai wani abu who will protect you and stand by you? Ayau dudda banda wani abu but at least I use strength dina na shiga gari ina neman wanda zai taimakeni ya tsayama diyata but randa bananan fa? Who will fight for you and stand by you? Lokaci yayi dazaki bar halin nan, ke kadai gareni kene komi nawa if something happens to you I die, jiya I was so scared…..” saikuma tafashe da kuka dayasa Rashida ta rungume Mamanta da gudu tace “Mama it’s okay bazan kara ba kinji, I’m here now I’m fine kinga kafan ma naji ya warke tass” ta shilla kafan sama Mama tace “maganin da Riyad ya siyamiki ne” haderai tayi da sauri tace “Mama wlh na tsaneshi baida kirki niyake gayama zai rabaki dani yana kirana selfish daughter” ahankali Mama tace “he did the right thing, kuma kika dameni zan bishi dagaske, Allah yamai albarka daya miki fada, naji dadi da akwai wanda zai iya miki fada haka kiyi shiru dan gani kike kaman kinfi karfin kowa” tashi tayi sabida bataso tace wani abu tasake batama Mama rai kawai tawuce tafita.

Alwala tayo sai yanzu ma ta Tuna ki ruwa batasha ba jiya to waka yasha? Har Mama ma batasha ba Tana salla tafita tea tahada musu sukasha sannan takaima Mama ruwan wanka tadawo tadawo ta gyara gidan ciki da waje tsaf Mama tace “zoki wanka karmu rasa sallan idi idan muka dawo mayi girki”.
Wanka awuce tayo tadawo atampanta na salla data karbo fara wajen dinki ta warware skirt da riga ne blue pink atampa ne tasaka da sabon bra da pant tayi kyau sosai dudda batai lalle ba daman jiya sukace zasuyi but Allah bai nufa ba, ta daura dan kwali Mama tace “zauna kisa kwalli ki shafa jan baki kodan darajan yau salla” batai musu ba tazauna tajawo basket na kayan kwalliya tadauki kwalli tasaka tadau wani pink tsohon jan bakinta ta shafa ta gyara gashinta wanda shi ta wanke abayi yanzu da safen nan ta shafa mai ta taje tai parking sannan ta daura dan kwali ta fesa turare ta tashi sai Mama dake kokarin sa hijabi tabita da kallo batasan lokacin datace “tubarkallah Allah ubangiji ya nunamin aurenki haka kici gayu kısa kayan amare” turo baki tayi taki amsawa tadauki pink hijabin data dinko na salla tasaka ta dauki dadduman su da yar wayanta suka fito rufe gidan sukayi da kafa sukaje masallacin ana salla ana kaiwa sujud Mama tashiga rokon Allah yabama Rashida mijin dazai sota ya tsaya mata yakuma kula da ita, sallamewa akayi suka wuce kasuwa kaji guda biyu suka sayo da kayan Miya da fulawa dasu butter sannan suka shigo keke suka tafi gida suna dawowa ta shiga kiciniyar hada gawayi dan daura abinci ganin gawayinsu saura kadan gashi tasa abinci a wuta yasa tarike kudi a hannu tawuce zaure dan neman yaro ta aika makotansu yakawo mata gawayi, tana sakai awaje karaf suka hada ido da Riyad daya bude kofa yafito daga cikin mota yana sanye da manyan kaya da babban riga da hula bugawa kirjinta yayi sabida yanda yayi kyau na bala’i, sai kawai ta tsaya chak ita takasa komawa ciki ita takasa motsi ita takasa daina kallonshi, har saida shi yadauke kanshi daga kallonta akufule yace “kifito yan duniya suga kwalliyan sallan da kyau!” Runtse idanu yayi dan baisan ya akayi maganan tafito daga bakinshi ba, saikuma yahade giran sama da kasa yajuyo yamata wani irin kallon da kawai taji tajuya da sauri takoma cikin gida kirjinta na bugawa dim dim dim chan sai ga sallaman yaro yashigo da kwalin kaji yace “gashi wai inji Riyad aba Mama” afadace Rashida tace “Kai maidamai kace batanan” yaron yace “ai yashiga mota yatafi” ranta taji yabaci daga daki Mama tace “ijiye zo ga tukuici” dasauri yaron ya nuna new 1k note dake hannunshi yace “ai yabani dubu daya” yajuya yafita abinshi, hijabi Rashida ta dauka tasaka tafita ganin bayanan yasa ta shiga makota tasayo gawayi tana dawowa taga Mama tacire just 3 acikin kajin da an gyara but ba’a yayyanka ba tace “dauka sauran kikai gidan Baba Liman kice kawo mana akayi karsuki karba” batai musu ba ta dauka tawuce takai a zaure tahadu da Liman yace “jiya naje kauye saida nadawo naji abinda yafaru Allah kiyaye gaba ki gayama Mamanki zan shigo anjima da yamma” gyadamai kai tayi tawuce ta koma gida lafiyayyen girki tayi tai dambun naman kaza ta soya some tai pepper chicken da some, tai jellof rice tai cincin around 4 tagama komi ta shiga daki ganin Mama duk bata wani cicciba yasa tace “Mama baki ciba” ahankali Mama tace “kaina kedan ciwo anjima ya sauka zan sha” kallon Mama tayi saikuma ta zauna kusada ita tace “Mama kedai sabida ina chan ina aiki ne yasa bakiciba, bude bakinki kiga” ta deba rice din takai bakinta dan murmushi Mama tayi tabude ta karba just to make her smile ta yarda taci amman ko taste bataji na abincin ba.
Har isha’i hira sukeyi around 9 tai bacci awajen Mama tabita da kallo sannan ta lallaba ta mike tana dafa bango kujera ta dauka da buta tawuce chan bakin makwarara amai ta kwara sai ijiyan

zuciya takeyi ta wanke fuska tadawo daki kafafunta ta kalla da tun dazu da rana sai zugi suke mata gashi ta lura sunata kumbura, yanzu ma sun karu sai kawai ta zauna tai tagumi tana kallon Rashida damuwa da fargabanta data shigane yasa kawai taji jikinta yanaso ya rikice haryakai ga abinci ma bataso, tunani take, takasa manta maganan Jummai, dudda tahana Riyad karyay involving kansa a case din tasan yanda aka ciro Rasheedan nan that woman will find a way ta cutar da Rashida Alkawari ne wannan! She's just scared for yarta, idan tafita school aka dauketa fa? Idan aka halakata fa? Idan tasa akama Rashida wani abu fa? Wat if she set Rashida up yanzu ta yanda zata tura mata yarinya prison inda ko Riyad bazai iya cirota ba, abinda ke kara firgitata is zuciyan Rashida just like yanda tazo jiya ta takali Rashida and she fell for it still haka zata karayi Rashida kuma ba hakuri taje tai wani abu shikenan akamata akai prison with concrete evidence. Yaya zatai protecting Rashida? Kodai su saida gidan su koma kauyensu dudda Kawu ya koreta ada dasuka je? But makarantan Rashida fa, itafa asibiti fa, auren Rashida fa? Riyad fa? Batama Rashida kwadayi tai auren kauye, tanaso diyarta tazama wata babba aduniya, but idan matan nan ta turo maza suka dauke Rashida sukai amfani da itafa suka lalata mata rayuwa tunda dai burinta na police station bai yuwuba, tayaya zata kare yarta? Dudda Rashida akwai karfi akwai zuciya but maza maza ne! Idan akai kidanapping Rashida yanzu yaya zatayi? Tunani daban daban take sai kawai jikinta yasake rikicewa har aka kira asuba yau takasa tashi tana wajen zaune tana kallon yarta,har Rashida ta farka da kanta tabude ido taga Mama murmushi tayi tai mika ta tashi tace "Mama baki tadani ba sabida ba aiki ko" gari yawaye Mama banyi salla ba".
[5/18, 10:18 PM] +234 708 918 4042: 💫 SANYI DA ZAFI 💫

✍🏻M SHAKUR

EPISODE 2️⃣2️⃣

M SHAKUR INTIMACY CLASS NA MATAN AURE🔥🔥
M SHAKUR INTIMACY CLASS MUN FARA LECTURES FROM SCRATCH SEE I TEACH MY STUDENT REAL KNOWLEDGE.

SABIDA CLASS DIN NA SHEKARA GUDA CUR NE MUN FARA LECTURES FROM SCRATCH DAGA FARKO.
AMARE CAN JOIN THE CLASS ALSO.
YAU MUNYI MAGANA KAN SEX DA CLASSIFICATION OF SEX!

TRUST ME YOU CAN NEVER REGRET JOINING CLASS DINA I TEACH AND WE HAVE FUN DINA STUDENT DINA WHILE LEARNING.

JOIN US TODAY WITH JUST 5k FOR ENTIRE SHEKARA. TELEGRAM CLASS NE KIKA SHIGA ZAKIGA ALL ABUNDA NA KOYA, COME LEMME TRAIN YOU KI XAMA MATAN

NOVEL A IYA S*X🔥

FOR THOSE DAKE TUNANI ISKANCI AKE KOYARWA A CLASS DIN YOU ARE WRONG.

A INTIMACY CLASS I TEACH SEX EDUCATION HOW TO KNOW YANDA DA ABUBUWAN DA AKEMA MIJI IN SEX LIFE NAKU❤️

I WILL STILL TEACH A PORTION NA KISSA❤️

AKWAI PROGRAM CALL TALK AND HEAL WATO KIYI MAGANA KI WARKE! MEMBERS SHARE MATSALOLINSU KO A GROUP KOTA PRIVATE MUBAKI SHAWARWARI.

JOIN NOW!! NOBODY IN YOUR HOUSE ZAI IYA ZAUNAR DAKE YA KOYA MIKI ALL THIS🔊

PAY FOR YOUR NEWLY AMARYA DAUGHTER OR SISTER🔊🔊

5K FOR SHEKARA DAYA GABAKI DAYA❤️💃

SO MANY OF YOU BAKU IYA KOMI BA SAI GULMA DA ZAGINA😂

YOUR HUSBAND NAJIN HAUSHINKI CUS YOU ARE TRASH A BEDROOM AKUMA IYA KISSA 😂

MY DEAR DROP THE HATE AND COME AND LEARN HOW TO BE A BADDIE AWAJEN OGA💃💃💃💃

CHAT ME UP NOW AND JOIN THIS CLASS..
+2347012181461

Dasauri ta tashi tafice alwala tayo tashigo agurguje tasa hijabi ta tada salla tana sallamewa daganan kan daduman ta hango kafan Mama yanda suka kumbura suntum dawani irin sauri ta taso tazo wajen tace “innalillahi” dan yatsa tasa ya nitse akafan yanda jikin Rashida yahau rawa saida ta tsorata tace “Ma…..m” tama kasa magana tsabagen yanda zuciyanta ke bugawa saikuma ta juya a haukace zata fita daga dakin hijabin dake jikinta Mama takama hakan yasa da sauri tajuyo saikuma ta duka, ahankali Mama da bakinta baya motsi sosai tace “kaini nai fitsari nai alwala nai salla” gyadamata kai Rashida tayi da sauri tace “to Mama” tawuce tafita takai ruwa bayinsu sannan tadawo daukan Mama tayi ta dagata Mama ta tashi kafan natama nitsewa yake dasauri Rashida ta zaunar da ita tace “Mama  tsaya nakawo po kiyi fitsarin adaki namiki alwala” ta zaunar da ita tacire hijabin ta ijiye tafice taje chan hanyan bayi ta dauko po ta wanke tadawo dakin da taimakonta Mama tayi tai tsarki tadauko tafito tadawo ta goge wajen tass sannan tamata alwala ta daura ta kan dadduma dantai salla hannunta Mama takama tamata murmushi tace “relax babu abinda zai sameni daga hannunki inajin yanda zuciyanki ke bugawa” kallonta Rashida tayi idanunta sun cika da hawaye baki tabude zatai magana saita

kasa tafashe da kuka tace “Mama wlh ina sonki Mama, Mama kene rayuwana gabaki daya Mama kiyakuri kiji sauki I know damuwana yasa BP ki yatashi bare naje nakira Musa yaron Baba Liman ya kaimu asibiti, Mama kiyafemin wlh wlh wlh bazan kara saki magana ba, Mama kina cewa nabari nabari kinji Mama wlh na rantse da Allah” dayan hannunta Mama takai saman fuskanta ta goge hawayen dasuka zubo ahankali Mama tace “come” matso da fuskanta tayi kiss Mama tamata a goshi muryanta chan kasa tace “I love you Rashida remember this always konai fushi dake bahar zuciyata bane kinji, stop crying I will be fine muje asibitin jeki kira Musa” tai maganan tana kara goge mata fuskan tass tashi Rashida tayi tadauki hijabinta tafice daga gidan, gidan Baba Liman tawuce a kofar gidama taganshi ganinta yasa kafin tamayi magana yace “lafiya?” Ahankali tace “Musa nazo kira yakaimu asibiti jikin Mama yatashi” ahankali Baba Liman yace “Subhanallahi Allah yabata lpy jeki kimtsa zan biyoshi muzo” juyawa tayi takoma gidan Mama nakan dadduma kallonta tayi da kafafun dasuke amike kaman kara kumbura suke every minute, wata yar jakarsu ta dauka ta shiga debama Mama su t-shirt da zani she’s a student doctor she know case din Mama is not something daza’a sallamesu gobe, tadau zanin gado wankakke da hijabi itama tasa yan kayanta dan daga wajen zata dinga zuwa department dinsu ta kwaso duka kudin dasuke dashi tashiga kirgawa gashi sun kashe kudi akasuwa ranan salla, Mama sai kallonta take yanda jikinta ke rawa kaman tamata kuka tadai daure bataso ma tanuna mata kalan azaban datakeji saisa take daurewa sunayen Allah akwai take kira abakinta, 85k sukedashi tadauki wayanta tanada about 51k a account, jakan makarantan da da komi keciki tagoya ta gungura jakan takawo tsakar gida daidai lokacin an buga gate dasauri ta gungura box din waje su kasa a keke ahankali tace “Musa zoka tayani mu dauketa bazata iya tafiya ba” daga Musa har Baba Liman biyota sukai ciki, Baba yakalli Mama da idanunta ke a kulle sabida tsananin ciwo yace “sannu da jikin Maman Rashida sannu” gyadamai kai tayi batare data bude idanubta ba, Baba Liman yace “kawomin ruwa Rashida namata addu’a” dan yana ganin Mama yasan ita kadai tasan metakeji, kawomai ruwa tayi da sauri karba yayi yayi addu’o’i ciki yabata yace “bata tasha ki shafa mata sauran akafa” karba tayi cike da tsantsan so tace “Mama sha Baba Liman yamiki addu’a” ahankali Mama tabude idanunta dasukai jazur tadaurasu kan Rashida tadan bude bakinta kadan samata ruwan Rashida tayi tasha kadan sannan ta tsiyaya a hannunta ta shafa mata a kafafun sannan ta ijiye a gefe tace “Musa zoka tayani” zuwa yayi atare suka daga Mama tsaye sannan suka dauketa chak suka fita da ita a keke suka sata dawowa ciki tayi tadan gyara ko’ina agurguje sannan tadauko key tafito ta kulle gidan da kofansu tazo tashiga keke tazauna Musa yatada keken Baba Liman yace “duk yanda ake ciki kinkirani, Allah baki lpy Maman Rashida” Ameen Rashida ta amsa Musa yaja keken itakuma tashiga kiran HOD nata wacce suke kira da Mrs Bugaje wacce take Doctor Mama, kusan a kira nabiyu ta daga sabida girkin salla yau yawon salla, tana dagawa tace “Rashida how are you sorry ina kitchen ne I missed call naki is everything fine”? Ahankali tace “Ma jikin Mama ne kafafunta sun kumbura sosai she’s in pain muna hanyan tafiya hospital” Dasauri Dr Bugaje tace “take her to A & E, she must be treated as emergency, bari I will call Dr Usama yau ina off but I will come once na gama girki for my family, don’t worry okay Maman ki will be fine” gyadamata kai Rashida tayi tana sharce hawayen dakeson zubomata daga idanu sannan ta katse wayan, suna kaiwa asibiti A & E tawuce ba’asa sun jira anything ba sabida Rashida is a Dr aka sa Mama agado akai ciki da ita Dr Usaman yazo Rashida takasa komi, all ciwon Mama tadamata da hankali yake but hakanan she’s getting a special vibe daga wannan kaman zaifi

kowannne worst duba da kafafunta tana tsaye inda yagama dubata, sannan yajuyo yakalli Rashida Dr Usama yazo yace “follow me” binshi tayi ahankali har zuwa office nashi saikuma yajuyo ya kalleta dan murmushi kadan yamata cikeda hikima na manya yace “calm down Dr Rashida sit” tana tsaye tace “tell me meke damun Mamana Dr” Dr Bugaje warned him about telling her anything yabari saitazo hakan yasa yace “is just blood pressure ta yatashi” tana kallon kwayan idanunshi tace “tell me I can handle anything I know People living with HIV (PLHIV) dakuma HBP (High blood pressure) Hypertension sunada significantly high risk of cardiovascular events abubuwan daya danganci matsalan ciwon zuciya da mutuwa, which is thought to be due to a complex interplay of various factors including immune dysfunction, endothelial dysfunction, and inflammatory changes, nasan Mama na is at risk of coming down da stroke, heart attack, heart failure, kumburin jijiyoyin daukan jini na jikinta, taushewan vessels dake daukan jini daga zuciya zuwa jiki, kidney issues, high cholesterol, dakuma matsalolin iya numfashi” hijabinta takama tadaura daura kan fuskanta tana matse idanunta sosai dakeson suyi kuka tace “just tell me wanne daga ciki ke damun Mamana?” Wlh ayanda yaga Rashida shi kanshi saiyaji bazai iya gayamata ba gwara Mrs Bugaje tazo tagaya mata, dan murmushi yace “I actually called you nagaya miki yanayinki din nan zai saka Maman ki cikin tashin hankali, calm down Mrs Bugaje is coming wuce kitafi” wani irin kallo tama Dr saikuma ta tashi tawuce takoma A&E din tazauna kan kujeran dake gaban gadanso takalli Mama da idanunta ke kulle sai bakinta daketa motsi na la’ilaha illallah tanashan azaba takai hannunta takama tarike gam, kawai she’s just looking at Mamanta feeling pains she wish itane akan gadon kwance ta dauke ciwon instead of Mamanta, tana zaune awajen wayan jakanta yashiga kara na Mama cirowa tayi taga Liman dauka tayi takai kunne yace “Yaya jikin nata me akace Rashida?” Ahankali tace “Dr Bugaje nake jira tazo gatanan a hanya” anatse yace “kome ake ciki ki kirani Allah bata lpy” ahankali tace “Ameen ta katse wayan” ta ijiye.

Around 12 Mrs Bugaje tashigo office nata tafara zuwa ta ijiye bag nata da komi ta sanya lab coat tafito Babban mace ce dazata kai 50yrs haka office na Dr Usama taje tadan jima kafin sutaho ward din tare Rashida na zaune rikeda hannun Mama taji muryan Mrs Bugaje cikeda wasa irin na professional Doctors din nan tace “Mama yaya mukayi ni da ke?

Wat was our agreement? Dasauri Rashida ta juyo ta kalleta, handglove tashiga sawa tana murmushi tana kallon Mama kaman irin nothing serious din nan sannan tataho gaban gadon tace “open your eyes for me Mama kar Rashida tafashemin da kuka anan dukta damu” ahankali Mama tashiga bude idanunta da kyar tabude kadan sunyi jazur takalli Rashida dake tsaye gefen Mrs Bugaje tai zuru zuru bakaramin dadin hakan Mrs Bugaje tajiba tace “good job Mama, tell me meke damunki? Meya tadamiki da hankali haka dahar kika bata agreement namu na bazaki dinga tunani be?” Mrs Bugaje tai maganan tana duba kafafun Mama tana dubawa kumhurin yanzu ya wuce guiwowinta ma, cikin wani irin murya da baya fita Mama tace “Jummai, Jummai zata halakamin rayuwan yarinyana, Jummai nason halakamin yarinya” dasauri Rashida tai wajen takama hannunta da sauri tace “Mama dama abinda kiketa tunani kenan babu wacce zata iyamin komi I can defend myself kinji kidena tunanin” girgizakai Mama tayi hankalinta nawani irin tashi takalli Dr tace “Mrs Bugaje hide…….hide my daughter…..banson ta cutarmini

